

EYN GOSPEL TEAM

LITTAFI BINCIKE MAI TSARKI
(TA 6)

KAN BINCIKE

# KAFAFFE DA KUMA GINANU A CIKIN KRISTI

Kolosiyawa, 2:6-7



# GABATTARWA NA BINCIKEN

Ana maku maraba da zuwa binciken Littafin namu na bincike akan wannan magana "Karfaffa da Ginane akan Krisiti," wanda aka samu izawar ta daga cikin Littafin Kolosiyawa sura 2:6-7. Wasikar Bulus Manzo zuwa ga Kolosiyawa ta bada muhimman sani akan rayuwar Krisita a matsayi matafiye. Wannan misalign "karfaffa kuma ginanen acikin Krisiti" tana nunawa a fili cewa girma acikin Ruhu da natsuwa, tana bayana zahirin mahaɗin mai bi da Krisiti. Wannan babbin ta nuna muhimmancin karɓar Krisiti Yesu ya zama Ubangijin mu kuma ta zama ginsikin abinda ya taɓa rayuwar mu acikin wannan tafiyar Krisitanci. Riken tushin bangaskiyar mu ta zama da muhimmancin tsayawa daram kamar yadda Bulus ya ambata. Tunanin mu ta rataya ne akan yadda muke ɗaɗana rayuwa acikin Krisiti, wanda tana bukata kullum tare da niyyar dangataka wadda ta shafi kowane bangaren rayuwar mu.

A matsayin mu na masu bi, muna fuskanci kalubalai waɗanda suke sa bangaskiyar mu acikin gwaji. Karfaffawar Bulus tana iza bangaskiyar mu domin mu gwada (wannan bicikien) hanyoyin bada karfi ga abubuwan da muka bada gaskiya kuma mu yi tsayaya acikin tafiyar mu na Krisitanci. Wannan tana kai mu ne mu auna dangatakar da take tsakanin zuciya mai kodiya da kuma zuciya da take karfaffa da kuma ginane acikin sa.  Tunanin yadda godiya take zama shaida ga duniya. Wannan binciken kuma tana zurfafa sanin mu akan wannan baban kan magana.

Za mu kafa hankalin mu akan gane cewa karɓan Kristiti ba wai abinda zai faru sau daya tak kawai ba, amma mataki na fari ne na tafiya akan hanyar sa. Wannan misalin na abubuwan na "kafuwa da ginuwa cikinsa" tana kafa ganewa da tabbatacen tushe acikin Krisiti, da nuna kwanciyar hankali, karfi, da naciya cikin kallubalai na rayuwa. Ana koyarwa ma masu bi yadda zasu kafa kakarfan tushen koyaswa mara jijjiguwa da ka'idodin Kristanci acikin bugun littafi binciken.. Saboda haka, yayinda za mu fasara waɗannan misalai na kafuwa da ginuwa acikin Krisiti, tattaunawar mu zata bincika zurfin dangatakar mu acikin Krisiti da kuzarin ci gaba da tafiyar mu acikin ruhaniya.

## BINCIKE TA 1

# SAIWA

**Irimiya 17: 7-8**

### GABATTARWA

A fanin ilimin aikin gona, saiwa ita ce ɓangaren itace da ta kafu acikin kasa. Waɗansu tsire-tsire, kamar itacen oak tana da saiwa mai zurfi, yayinda waɗansu kamar ciyayi ba su da saiwa masu zurfi ba, kuma ba za su iya rayu ba indan ba'a basu ruwa akai akai ba. Idan tsire-tsire ba su da saiwa masu zurfi ba, za'a iya gan su kamar ba su da damuwa ba na dan lokaci, amma ba da dadewa ba, za su bushe su yankwane. Ba za su iya daɗe a lokacin fari ba. Saboda haka, ɗaya daga cikin abinda zai shafi daɗewar itace, ta dangana ga zurfin saiwar ta.

Saiwar kuma tana iya nufin ainihin tushen, dalilin, ko kafuwar abin. Kowane mutum yana da tushe ko saiwa (Zuriya). Zuriyar mutum tana iya shafi rayuwar sa domin tana ɗauke da rayuwa da halaye na kakannai, mai kyau da mara kyau. A yawancin al'adun mutanen Afrika, idan wani yana shirin yi aure, dole ne a yi bincike akan iyalan mai auren domin a sa tushen su. Ana yin wannan ne domin a kawar da samu mumunan halaye daga wata iyali. Ko Littafi Mai Tsarki ma ta binciko tarihin iyalin Yesu na duniya daga Yesse (Ishaya 11:1)

Tushen mu yanzu shi ne Yesu. Tun lokacin da muka karɓe shi ya zama Mai Ceto da Ubangijin mu, an maye haifuwar mu daga Iblis zuwa Yesu Krisiti. Domin mu iya gane abinda kan maganar mu take nufi sosai, dole mu bincika tushen mu wanda shine – Yesu domin mu iya sani inda muka fito.

### TATTAUNAWA

- Mene ne ake nufi da saiwa/tushe?
- Mene ne kake tunani zai faru da itace wanda bata da saiwa mai zurfi? Kuma mene ne zai faru da itace da take da saiwa mai zurfi?
- Me ya sa muke kwatanta Yesu da Saiwa?
- Mu tattauna dalilai da itatuwa da aka dasa su a bakin ruwaye ganyaye su kore ne kullum. Ta yaya za mu iya misalta wannan da rayuwar mu na Krisita (Irimiya 17:7-8, Zabura 1;1-3?
- Wane ne Yesu? Ta yaya ya zama saiwa/tushen mu (Matta 16:13-20, Kolosiyawa 1:13-14, 2:6?

## KAMALAWA

Ma'anar da aka samu daga cikin waɗannan kwatancin misalai tsakanin mutumin da ya dogara ga Ubangiji ne da kuma itace da aka dasa shi a bakin ruwaye. Misalin itacen da ya sa saiwar sa acikin ruwa tana ba da ma'ana mai zurfi ta ruhaniya, daidai da dogara ga Ubangiji, wanda take bada ciyarwa, karfaffawa a lokacin wahala, cin gaba da girma a ruhaniya da kuma kubutarwa daga alhini. Tana nufi cewa, waɗanda suka dogara ga Ubangiji, suna ɗaɗana zurfafan tabbataccen tushen ruhanniya, inda suna samu ci gaba da rayuwa ta wurin dangatakar su da Allah. Wannan dogara

## BINCIKE TA 2

# MUHIMMANCIN SAIWA GA ITACE

**Ayuba 14:7**

## GABATTARWA

Saiwar itace tana taimaka kaiwa itacen ruwa da abinci mai gina jiki ma itacen da resan da jijiyoyi. Kamar yadda jiki ba za ta iya yin aiki in ba tare da zuciya ba, haka kuma itace ba za ta iya rayu idan babu saiwa ba. Ayuba ya gaya mana cewa mudin idan saiwar itace tana acikin kasa, akwai sa zuciyar rayuwar sa, ko da shi ke an yanke ta. Yesu ya gaya mana a fili cewa shi ne itacen inabi, mu ne reshen, idan ba tare da shi ba, ba za mu iya mu rayu ba. Idan muna bukata ci gaba da rayuwa, dole ne mu rayu ta wurin koyaswan Yesu. Yahaya 6:48-51.

## TATTAUNAWA

- A tattauna muhimmancin saiwa ga itace
- A karanta Yahaya 15:1-6, Ayuba 14:7 kuma a tattauna yadda Yesu yana da muhimmanci ga Krisita/masu bi
- Akwai wađansu itatuwa da suke rayuwa a hammada, yayinda wađansu kuma ba za su iya ba. A tattauna yadda wannan yake zama haka, kuma wađansu ba za su iya ba, kuma yaya za'a iya misalta wannan da rayuwar Krisita?
- Itace mai kyau zai iya bada yaya mara kyau? Ta yaya yake faruwa cewa ko da shi ke wađansu Krisita suna jin maganar Allah, amma har yanzu suna bada mumunan yaya (Galatiyawa 5:19-24)?

## KAMALAWA

Akwai resuna dayawa akan itace, amma saiwa iri daya yake ba su abinci gina jiki, kuma za su bada yaya iri daya. Idan mun ce mu Krisita ne kuma rayuwar mu bata nuna hasken Yesu ba, to, za mu iya ce muna samun abinci gina jikunan mu daga wani wuri daban, ba daga wurin Yesu ba.

## BINCIKE TA 3

# SAIWA TA RUHANIYA

**Luke 8:4–15**

### GABATTARWA

Saiwa ta ruhaniya ita ce karfin mai bi. Wannan ne alamar bangaskiyar mu mara jijiguwa acikin Allah; ita ce kuma ginshikin abinda ya rike mu acikin gogorimayar wannan rayuwa, kamar yadda saiwa ta kan rike itace lokacin guguwar iska. A cikin misalin mai shuki a Luka 8: 4-15, saiwar tana misalta zurfin bangaskiyar mutum da kuma himmantuwa ga koyaswar Yesu. Yesu ya bayana irin kasa daban daban inda ake suka iri, wanda yana nuna irin maida martanani da ake yi ga mulkin Allah. Wannan misalin ta nuna yadda samun saiwa mai zurfi tana da muhimmanci. Samun saiwa mai zurfi tana samuwa ne daga cin abinci ruhu kowane rana. Ta shafi karanta maganar Allah, addu'oi da nazari akan sa dukan yini.

### TATTAUNAWA

- A ganewarka, mene ne saiwar ruhaniya?
- A tattauna misalin mai shuki nan bisa ga yadda mutane suke sauraron maganar Allah yau Ekklesiya Luka 8: 4-15
- Ta yaya za mu iya bunkasa saiwar ruhaniya ?
- Wane alamu ne za su nuna cewa mutum ko wani yana da saiwar ruhaniya ko a'a (Ibraniyawa 5:12-6:1-2?
- Mene ne abubuwan masu afani kuma za su afana idan akwai saiwar ta ruhaniya (Afisawa 4:14)?

### KAMALAWA

A wannan karshen zamani, kasancewar Anabawan karya da Malamai sun zama mana barazana rayuwa ta ruhaniya mai iganci. Idan ba tare da tushen rayuwa ta ruhaniya ba, muna acikin hatsarin baudewa. Kallubalai na rayuwa ma, za su iya janye hankalin mu daga bangaskiyar mu idan ba mu kafa saiwar mu ta ruhaniya da zurfi ba. Bari mu nemi jagorar Ubangiji mu ta kafu daram acikin koyaswan Yesu. Bari alherinsa ya sa mu tsaya ba tare da waiwayawa acikin iskar ruɗani da jan hankali, muna tabbatar cewa

**BINCIKE TA 4**

# LOKACIN DA SAIWAR TA BUSHE

**Yusha'u 9:16**

## GABATTARWA

Saiwar ba shaka ita ce ta fi muhimmanci a itace. Ita ce hanyar da ta wurinta ne rassan itacen suke samu abincin jina jikinta har ya kai zuwa ga resunan itacen. Idan an dasa saiwar sosai a kasa kuma ta samu isheshen ruwa, itacen ana zato zata bada yaya sosai. Haka kuma, itace bata iya rayuwa cikake idan saiwar tana akan idan akwai duwatsu kuma babu isheshen kasa da ruwa da zata samu ba. Rayuwar mutum zata zama busheshe (holoko) game da bada yaya da za su gamshi Allah. Muna addu'a cewa Allah zai taimake mu kirkiro dalilai da za su taimake mu tabbatar cewa babu abinda za su hana mu kafa saiwar mu acikin Allah ba.

## DISCUSSION

- 'Mene ne suke sa saiwa su bushe (Yusha'u 9:1, Yahaya 4:13-14)?
- Sau nawa ne muke gani halaye irin kasa mai kyau? Mata 13: 23; Zabura 1:3; Irimiya 17:8; Ezekiel 37:12 acikin Krisita?
- Ta yaya ne halaye busheshiyar kasa a Mattiyu 13:5 ta misalta rayuwar mu?
- Mene ne hatsarin busheshiyar itace bisa ga ruhaniya? Mattiyu 7:19-23, Luka 3:9?

## KAMALAWA

Allah ya hallaci mutum domin ya hayayafa ya riɓaɓanya. Wannan tana nufi cewa rayuwar mai bi kullum da laushi kullum tana girma tana bada yaya domin mutane su ci. Abinda ya zama saɓani da wannan, tana nufi cewa ana rayuwa ne wanda ba bisa ga shirin Allah da manufarsa ba. A matsayin mu na Krisita, Allah yana kira mu da zama da ganyaye masu bada yaya domin sunan sa ta sami daukaka ta wurin mu.

## BINCIKE TA 5

# KAFFAFE ACIKIN KRISITI TA 1

**Romawa 11:17**

## GABATTARWA

Dasawa da Bulus Manzo ya yi afani da shi anan kwatanci ne mai ma'ana ta ruhaniya akan irin dangatakar da ke tsakanin Al'ummai masu bi (Zaitun na jeji) da Yahudawa (Rassan Zaitun). Manufar wannan ita ce Al'ummai masu bi an sa su zama ɗaya da Yahudawa acikin alkawarai da albarkun Allah. Tsarin dasawa tana bayana alkawari Allah da ta shafi kowa, wadda bata tsaya akan mutanen farko da aka yi masu alkawarin ba amma ya hada da sauran al'umma. Wannan ta kara jadaɗa tunanin cewa ceto tana samuwa ga dukan waɗanda suka bada gaskiya, babu banbancin kabila ko al'adu. Yesu yace, "Ni ne itacen inabin, ku kuwa rassan." (Yahaya 15:5). Wannan a bayane ta ke duk lokacin da mutum ya samu ceto, rayuwarsa ko al'amuransa a nan duniya bata zama bisa ga rayuwa ta halita ko kuma tushen asalinsa ba, amma bisa ga saiwar ta ruhaniya (Yesu Krisiti). Wannan tana nufi cewa wanɗanda suka samu ceto an dasa su acikin rayuwar Krisiti. Dassashe tana nufi cewa maganar Allah tana zaune acikin mu. Tana nufi wannan ita ce burin mu, karfi ta ruhaniya, da kuma rayuwa cikin ruhaniya ana samun ta acikin Yesu.

## TAMBAYOYI DOMIN TATTAUNAWA

- Mene ne ake nufi da kafuwa acikin Krisiti?
- Mene ne ake nufi da ci gaba da rayuwa acikin Krisiti?
- Idan ku zauna acikina, ni kuma acikin ku, zaku bada yaya. Wane irin yaya ne Yesu ya ke nufi annan?
- Mene ne zai faru da waɗanda suka ki bada yaya ko kuma su kasance acikin Krisiti (Yahaya 15:6-7
- Mene ne afanin kasancewa acikin Krisiti (Yahaya 15:7)?

## KAMALAWA

Muna bukata a dasa mu acikin Krisiti domin kada mu dinga lilo idan guguwa ta bugo hanyar mu. Mai yiwa ne mu yi lilo nan da can domin iskar, amma idan an dasa mu acikin sa sosai, babu wata iska da zata jijiga mu ba.

**BINCIKE TA 6**

# KAFFAFE ACIKIN KRISTI TA 2

**Kolosiyawa 2:6-7**

## GABATTARWA

Wurin da muka karanta yana bukaci masu bi domin su ci gaba da tafiyar su acikin Krisiti, kaffafe sosai acikin sa, suna girma acikin bangaskiya, suna nuna godiyar su domin ikon da yake acikin Bishara domin sake rayuwar mutane. Ya jadaɗa muhimancin samun kakarfan tushe acikin Krisit da cin gaba acikin kyakyawan dangataka acikin sa. Yin afani da misalin girman itace ta zama da muhimmanci ganewa afanin zama "karfaffa acikin Krisiti". Kamar itace karfaffa, saiwar da suke acikin kasa sune suke rike da ita, suna baiwa itacen karfin da zata yi tsai har ta bada yaya. Haka ma, zama karfaffa acikin Krisiti tana bukata samu tushe acikin koyaswan sa. Mane kan mu ma Yesu tana nuna cewa mun zama ɗaya da shi a cikin jiki da kuma zurfaffan bangaskiya mara jijiguwa da dogara gareshi. Wannan naciyar kafuwa tana bayana juriya, tana hana mu girgizuwa ko kuma juyawa lokacin da muke fuskanci gwaji ko tsananin rayuwa.

## TATTAUNAWA

- Ta yaya za mu zama karfaffu acikin Krisiti?. Kol. 2:6-7, Romawa 6:3-11?)
- A tattauna addu'ar Bulus ma Mutanen Afisa cewa Krisiti ya kafu a zukatan su ta wurin bangaskiya kuma su zama karfaffu acikin kauna. Afisawa 3:16-20)
- A tattauna muhimmancin karfaffuwa acikin Krisiti.,
  i. A tsaya da karfi acikin gwaji
  ii. Mabuɗin bada yaya (Yohanna 15:4-8),
  iii. Mu iya gane gaskiyar managanar Allah domin kada a rude mu. Mattiyu 24:4-5, 10-12
- Wannan tana nuna cewa ba za mu fuskanci kallubalai ba idan mu kafu acikin Krisiti? Yohanna 15:18?

## KAMALAWA

Ana jadaɗa cewa abu muhimmi ne ga Krisita mai bi ta musaman mai son shaida Bishara ga waɗanda basu bada gaskiya ba, su zama karfaffu acikin Krisiti. Girman mu acikin Ruhu da bada yaya suna bukata kafuwa sosai da tushe mai kyau acikin Krisiti. Wannan, ita ce ake nufi da karfafuwa acikin Krisiti.

**BINCIKE TA 7**

# ANFANIN ZAMA KAFAFFE A CIKIN KRISTI

**Galatiyawa 5:22-23, Zabura 1:1-3, 6**

## GABATTARWA

Waɗansu daga cikin afanin da za'a samu yayinda muka zama karfafu acikin Krisiti Yesu su ne mu zama acike da iko da zamu iya yi tsayaya da guguwar wannan rayuwa, kamar mutumin nan mai hikima wanda ya gina gidan sa akan dutse. Kowace gugguwar iska koyaswa da ruɗun mutane baza su ɗauke su ba domin jin daɗin bincike da nazarin maganar Allah da suke yi kullum. Kuma Ubangiji yana lura da alamuran su kullum. Ga irin waɗanan mutane, kowane abu mai yiwu wa ne, kuma su masu farin cikin ne domin suna da farin ciki da kwanciyar hankali, domin sun sani saiwar su na kafe da zurfi acikin Krisiti domin su iya jimire lokacin fari wanda zai ciyar da su domin su bada yaya a lokacin ta. Zama kafaffe acikin Krisiti tana sa mu ci gaba da girma muna cika manufar rayuwar mu da tuni cewa, "Mu aikinsa ne, an sake halittarmu a cikin Almasihu Yesu musamman domin mu yi kyawawan ayyuka," Afisawa 2:10. Nufin Allah domin kowane mai bi shi ne domin ya zama da gaba gaɗi akan cetonsa ko centonta. Shi ya sa waɗanda suke karfaffe acikin Krisiti za su iya ce."Domin ni, a gare ni, rai Almasihu ne, mutuwa kuwa riba ce." (Filibiyawa 1:21). Yayinda za mu shiga cikin tattaunawa, bari dukan mutane su gane muhimannci da afanin da suke tatare da karfaffuwa acikin Krisiti. Amin.

## TATTAUNAWA

- Ta yaya mutum zai iya zama karfaffe acikin Krisiti kafin ya ɗaɗana afanin sa. Misalai 3:5; Zabura 1:1-3, 121:1, 2Kor. 5:17?
- A tattauna albarkar Ruhu Mai Tsarki bisa ga Galatiyawa 5:22-23, muna kwatanta afanin sa da zama karfaffe acikin Krisiti.
- Ko waɗanda ba masu bi ba ma za su iya ɗaɗana afanin abubuwan da muka lissafta acikin gabattarwar mu? Idan haka ne, ta yaya?, Idan ba haka ba, me ya sa?
- Ko ka zama karfaffe acikin Krisiti kuma kana ɗaɗana afanin sa?

## KAMALAWA

Afanin zama karfaffe acikin Krisiti ba za mu iya wuce gona da iri ba. Ana bukata ka kudurta ka bada kai da Ruhu Mai Tsarki ya dauki mazaunin sa acikin ka. Yana sa mutum ya ci gaba da samu abincin maganar Allah ta wurin bincike da nazari akan sa dari da rana. Yana sa mutum ya karfaffu acikin Ruhu, ya zama da gaba gaɗi da karfin hali.

**BINCIKE TA 8**

# RASHIN GANEWA AKAN ZAMAN KAFAFFE ACIKIN KRISITI Kolosiyawa 2: 6-7

## GABATTARWA

Acikin tafiyar mu na rayuwa acikin Krisiti, akwai waɗansu abubuwan da muka bada gaskiya a garesu, yayinda muka yi bincike sosai, muna iya gano cewa akwai rashin fahimtarwa. Bari mu bincika waɗannan rashin fahimtarwa tare sa'anan za mu samu a bude mana gaskiyar da ta zama tushen cibiyar zama kafaffe acikin Krisiti

## TATTAUNAWA

- **Rashin Fahimta: Zama Kafaffe Tana Bayana Zama Cikake (Kolosiyawa 2:6)**
  a. A tattauna irin rashin fahimta da take nuna cewa zama kafaffe acikin Krisiti tana nufi, rayuwa ta zama da sauki, babu damuwa kuma acikin rayuwa. (Kolosiyawa 2:6)
  b. A bincika gaskiyan zama kafaffe acikin Krisiti ta kunci girma, koya da dogara ga Krisiti acikin rayuwar ajizanci ko kasawa
- **(Rashin fahimta: Zama kafaffe tana kai ga girma acikin Ruhu nan da nan. (Kolosiyawa 2:6)**
- Mu bincika irin wannan bangasikar cewa zama kafaffe acikin Krisiti tana sa mutum ya yi girma acikin Ruhu nan take.
- A tattauna irin tafiya da girma acikin Ruhu da jimirewa da ake bukata masu bi su samu domin su samu saiwar su ta yi zurfi.
- **Rashin fahimta: Zama kafaffe acikin Krisiti ba abinda ake samu kullum ba. (Kolosiyawa 2:7)**
- A yi magana akan wannan rashin fahimtar cewa zama kafaffe acikin Krisiti abu ne da ya shafi mutum shi kadai, ya ɗaɗana kuma.
- Mu kuma tattauna yadda zama kafaffe acikin Krisiti ya shafi jama'a duka da muhimmancin zummunci a tsakanin masu bi.
- **Rashin fahimta: Zama kafaffe acikin Krisiti abu ne da zai faru sau daya tak. (Kolosiyawa 2:7**
- A tattauna wannan magana cewa zama kafafe acikin Krisiti abu ne da zai faru sau daya tak amma, ba abinda zai ci gaba da faruwa akai akai ba.
- A bincika yadda ci gaba da zama ana aiki tare da Krisiti yana da muhimmanci domin rayuwa zama kafaffe acikin Krisiti.
- **Rashin fahimta: Zama kafaffe tana tabbatar da wadata. Kolosiyawa 2:6**

- A tattauna wannan rashin fahimtar cewa zama kafaffe acikin Krisiti tana tabbatar da rayuwar wadata da nasara.
- A bincika daga Littafi Mai Tsarki bayanai da suka kalubalanci wannan rashin fahimtar sa'anan a nuna daga Littafi Mai Tsarki gaskiyan zama kafaffe acikin Krisiti ta kunci jimirewa alokacin da ake acikin walwala da lokacin shan wahala.
- **Rashin fahimta: Zama kafaffe acikin Krisiti daidai take da rayuwar jin dadi. (Kolosiyawa 2:7)**
- A yi magana akan wannan ra'ayin cewa zama kafaffe acikin Krisiti tana kai ga zama jin dadi, babu damuwa acikin rayuwa.
- Mu duba daga cikin Littafi Mai Tsarki da ta nuna cewa zama kafafe acikin Krisiti ta kunci mutum ya bar wurin jin dadi da yake yi domin aikin mulkin Allah da kuma rayuwar sa ta Ruhaniya.

## KAMALAWA

Bari wannan binciken ya zama hanya da zata kawar da wannan rashin fahimtar da haskaka zurfaffan gaskiyar zama kafaffe acikin Krisiti. Yayinda muke girma acikin sani, bari saiwar mu ta shiga da zurfi acikin kasar kaunar magana Allah da alherin sa, suna sa mu bada yaya dayawa mu kuma tsaya da karfi acikin gaskiyar maganarsa.

**BINCIKE TA 9**

# SHARUƊA NA ZAMA KAFAFFE A CIKIN KRISTI **Yohanna 3:1-10; Markus 8:34; 10:21**

## GABATTARWA

Domin mutum ya zama kafaffe acikin Kristi Yesu, shi/ita dole a wuce acikin lokuta na sauyi dayawa da abubuwan da ake bukata su sa mutum ya cancanta ya zama da karfi sosai domin wannan tseren ta Ruhaniya. Dole mu guje dukan abubuwan jin daɗi da suka makantar mana zukatan mu da tunanin mu. Ba shaka shi ya sa Yesu yace dole mu musunci kanmu. Waɗannsu muhimman abubuwanda ake bukata domin zama kafaffe acikin Krisiti Yesu su ne cewa an maye haifuwar mutum kuma an yi masa baptisma da ruwa da Ruhu Mai Tsarki kafin mutum ya shiga cikin mulkin Allah. (Yohanna 3:1-10). Ayyukan jiki duka sun mutu, waɗanda suke raba mu da Krisiti. (Romawa 8:13, 2 Tarihi 7:14.)

Bada kai da muke yi domin ayyuka masu kyau sune suke bayana irin bangaskiya da muke da shi acikin Krisiti. Leɓunan bakunan mu ba za su iya shaida ta kadai ba, amma bari ta fito daga birin zukatan mu. Kada wani abu mara zurfi na ruɗun duniya da koyaswanta su sa mu bauɗe; bari mu ci gaba mu karfaffa bangaskiyar mu acikin Krisiti. (Kolosiyawa 2:8)

## TATTAUNAWA

- Bisa ga ganewar ka, ka lissafta waɗansu abubuwan da ake bukata daga gareka kafin ka zama kafaffe acikin Krisiti)
- A tattauna yadda ya kamata da kuma dalilin da kamun kai, binciken kai, bada kai, naciya da jimirewa da sauran su, sun zama abubuwan dole ne domin zama kafaffe acikin Krisiti.
- Mark 10:19–24). (A tattauna dalilin da ya zama da wuya waɗansu masu bi, su bayar da dukiyar su domin Bishara duk da cewa sun zama masu bi na shekaru dayawa.
- **A tattauna yadda musun-kai yake a matsayin zama acikin Krisiti. (Markus 8:34; 12:29-31, Luka 14:26-27**

## KAMALAWA

Koda shike cetonmu an ce kyauta ne daga wurin Allah, wanda ya kaunace mu ya sa Ɗansa haifaffe shi kaɗai ya mutu akan giciye domin mu, ana kira domin mu karba da godiya, bangaskiya da biyaya. Ta haka, ga wanda ya karɓa dayawa, ana bukata dayawa. Wannan tana nuna cewa saudakar da kai na mu ga almajiranci ta kowane bangare tana da muhimmanci. Bari mu yi rayuwar mu acikin Krisiti dukan kwanakin mu. Amin.

# BINCIKE TA 10

# YADDA ZAMU ZAMA KAFAFE ACIKIN KRISITI

**Kolosiyawa 2:6 -7**

## GABATTARWA

A cikin gwagwormayar rayuwa na yau da kullum, da sauki ne mu iya fuskanci abubuwan da za su janye hankalin mu, amma Littafi Mai Tsarki yana kira garemu da mu zama kafaffe acikin Krisiti. Wannan Littafi binciken, tana sake sa mu yi binciken abinda ake nufi da kafa dangataka ta Ruhu mai karfi acikin sa. Tare, bari mu bincika Littafi Mai Tsarki mu iya gane a fili abubuwan da za su sa mu gina dangataka mai ɗaurewa da Mai Ceton mu.

## TATTAUNAWA

- **Kira domin karɓa Krisiti (Kolosiyawa 2:6; Yohanna 3:3; Yohanna 1:12, Afisawa 2:8**

  a. Mu yi tunani akan abinda ake nufi da "A karɓi Krisiti ya zama Ubangiji" yadda ya shafi rayuwar ka.

  b. Ko zaka iya bada shaida irin naka yanayin da ya shafe ka yadda karɓan Krisiti ya taɓsa rayuwarka ta Ruhaniya.

- **Tafiya acikin sa (Kolosiyawa 2:6; Yohanna 15:7; Ayyuka Manzani 17:28; Yohanna 15:3**

  a.Mene ne ake gani akan tafiya acikin sa kowane rana a rayuwa?

  b. A tattauna wannan ra'ayin cin gaba da dogara akan Krisiti acikin tunani, ayyuka da shawarwari da mu ke yi.

- **(Zama kafaffe acikin Krisiti (Kolosiyawa 2:7; Zabura 1:1-6, Galatiyawa 2:20)**

  a. Mu kafa tunani akan wannan misalin "zaman kafaffe da kuma ginanu acikin Sa." Mene ne ake nufi da zama kafafe acikin Krisiti?

- **Muna cike da godiya (Kolosiyawa 2:7; Zabura 107:8-9; Kolosiyawa 4:2; 1Thesalanikawa 5:16-18**

  a. Ka bincika ma'aunin da ke tsakanin zama kafaffe acikin Krisiti da rayuwa da take cike da godiya.

  b. Ka bada labarin yadda rayuwa da take kafaffe acikin Krisiti ta kai ga godiya a fanoni dayawa.

## KAMALAWA

Shawarar Bulus zuwa ga mutanen Kolosiyawa tana nuna mana cewa wannan jagora ce na kowane lokaci. Yana jadaɗa yada ake cigaba da

karɓan Krisiti, muna gani yadda tafiyarmu na canja rayuwar mu na "rayuwa acikinsa". Zama kafaffe acikin Krisiti tana nuna wata zurfin, tsayayen dangataka wadda take rayarwa, tana sa masu bi su fuskanci kallubalai masu yawa. Karshen wannan ita ce, rayuwa da take cike da godiya, wannan sakamakon bangaskiya da ta kafu a wannan tushen.

**BINCIKE TA 11**

# HALIN MUTUMIN DA YAKE KAFAFFE ACIKIN KRISITI Afisawa 3:16-17; Yohanna 15:5

## GABATTARWA

Zaman kafaffe acikin Krisiti ya zama tushen cin gaba da rayuwar Krisitanci. Ta shafi amencewa da shi ya zama Ubangiji da Mai Ceton ka kuma ka yarda koyaswan sa da kasancewar sa ta canja halayen mu da ayyukan mu. Yana da muhimmanci ga rayuwar mai bi ta fanoni girma acikin Ruhu da kuma balaga. Bangaskiyar mu acikin Kristi ba kawai ta tsaya ba amma rayeyen dangataka ce wanda ta taɓa kowace bangaren rayuwar mu. Zamma kafaffe acikin Krisiti ba wai kawai bada gaskiya ba, amma zurfafan dangataka mai ci gaba. Ta shafi rayuwa acikin Krisiti, muna samu karfi da ciyarwa daga gareshi.

Karshen tafiyar mu acikin bangaskiya bata tsaya akan ceto kadai ba., amma abu ne mai ci gaba, tafiya a gaban sa. Zamma kafaffe acikin Krisiti takan canja halayen mu da ayyukan mu; muna zama kamar Krisiti yayinda muke girma acikin sa, wanda takan kai ga rayuwa wanda take cike da godiya da girma acikin Ruhu. Rayuwa da ta kafu akan halin Krisiti takan canja yadda muke hulda da mutane ta jadaɗa kauna, gafara, da kuma sulhuntuwa. Dangatakan mu ta zama abin shaida ne na aikin Krisiti acikin mu.

## TATTAUNAWA

- Mene ne ake nufi da kafaffe acikin Krisiti? Ta yaya za'a iya banbanta shi da bada gaskiya ga Krisiti kawai? ( Kolosiyawa 2:6-7)
- Ta yaya zama kafaffe acikin Kristi zai taba rayuwar mu na kullum ta wurin halayen mu da ayyukan mu? (Galatiyawa 5:22-23?
- (Ta yaya zamu iya karfafa junan mu masu bi domin mu iya zama kafaffu acikin Krisiti?
- Bisa ga Afisawa 3:16-17, mene ne hakin Ruhu Mai Tsarki acikin taimakon mu domin mu zama kafaffu acikin Krisiti?
- Acikin naka kalmomin, ka bayana banbancin da ke tsakanin mutum wanda yake kafaffe acikin kaunar Kristi da mutumin da ba ya kafu acikin kaunar sa ba.

## KAMALAWA_

Zama kafaffe acikin Kristi ba wai abinda zai faru sau daya ba, ama zarafi ne domin cin gaba da girma da canjawa. Halayen mu, da tunanin mu, da dangantakar mu za su bayana kaunar sa yayinda muke rayuwa acikin sa. Bari mu zama kafaffu acikin Krisiti, muna samun karfi daga gareshi kuma muna bada yaya irin waɗanda rayuwarsu ta kafu akan halayen Krisiti.

## BINCIKE TA 12

# ALAMA DA TAKE NUNA CEWA AN ZAMA KAFAFFE ACIKIN KRISITI

**Mattiyu 7:16. Galatiyawa 5:22-23**

### GABATTARWA

Ana fada cewa an fi gane mutum ta wurin ayyukansa fiye da maganarsa. A matsayin mu na masu bin Krisiti, rayuwarmu ya kamata ta shaida irin ikon sakewar da muka samu ta wurin zama kafaffe acikinsa. Bari mu bincika tare acikin Littafi Mai Tsarki domin mu gane kwararan alamomin da suka nuna sahihiyar dangatakar namu da Mai Cetonmu.

### TATTAUNAWA

- Bisa ga Kolosiyawa 2:6-7, a wane hanyoyin ne kake tsamani zama kafaffe acikin Krisiti ya banbanta da bada gaskiya acikinsa?
- Za mu yi afani da Yusufu, Ibrahim da Ayuba acikin binciken mu, bari mu fada sahihiyar misalai yadda mutum zai iya nuna zama "kafafaffe da ginanu acikinsa" acikin ayyukan su na yau da kullu.
- Mu tattauna irin kallubalai da mutum zai iya fuskanta acikin rayuwansa na zama kafaffe da kuma mu yi magana akan irin dabaru da zamu iya cin nasara akan su.
- Ta yaya amencewa da Kristi a matsayin Ubangiji zai iya shafi irin yadda muke gani manufarmu da abubuwan da muka basu fifiko?
- Mu auna diyan Ruhu acikin Galatiyawa 5:22-23, ta yaya irin wadannan halayen zasu zama shaida da za'a gani ta ainihin dangantar mu da Krisiti?

### KAMALAWA

Yayinda za mu kamala wannan binciken, bari mu samu izawar kakarfa da gaskiya cewa rayuwarmu zata iya zama shaida na zaman mu kafaffu aciki Krisiti. Bari wadannan tabbatacen shaidar da muka tattauna – muna rayuwarmu da bangaskiya, muna tafiya acikinsa, muna bada yaya Ruhu Mai Tsarki, muna nuna biyaya da saudakar da kai – su zama a bayane acikin rayuwarmu kullum acikin tafiyar mu tare da Krisiti. Bari rayuwarmu ta zama takamamin shaidar ikon sakewar zaman mu kafaffe acikin kauna da alherin Ubangijinmu da Mai Cetonmu Yesu Krisiti.

**BINCIKE TA 13**

# KALLUBALAI NA ZAMA KAFAFFE ACIKIN KRISITI 2Timoti 3:10-13; Yohanna 15:18-21

## GABATTARWA

Mu sa wannan acikin tunanin mu cewa hanyoyin mu cike suke da kallubalai duk lokacin da muke shaida Bisharar Yesu Krisiti. Yayinda muke fuskanci waɗannan kallubalai masu karfi da suke sa mu jin tsoro kullum da kuma su raunana bangaskiyar mu acikin Krisiti, kaito waɗansu mutane sun koma da baya sabili da wannan, wanda har ya kaisu da barin Bishara. Yesu bai bar mu acikin duhu akan wannan ba, amma har ya gargaɗe mu kafin waɗannan kallubalai su adabe mu. An tsanata ma Ubangijinmu Yesu Krisiti har ya kai shi da mutuwa. Idan ba tare da kaucewar sa ba, za mu sha tsanani irin da ya sha domin Bishara. Duniya ta ki shi da fari domin shi bana duniya ba; haka mu ma ba na duniya ba. Muna rayuwa a duniyar da tana da iko akan rai, amma ikon tsayaya da wannan ikon har karshe ita ce ta fi muhimmanci.

Bulus Manzo ya taɓa umarci abokin aikin sa Timoti game da kallubalai da ya fuskanta a Antioch da Lystra. An tsanata masa amma, ya jimire, kuma Ubangijinmu Yesu Krisiti ya cece shi daga abokan gabansa. Rayuwa ta adalci acikin Krisiti ita ce sahihiyar rayuwar musun kai. Albarka ta tabbata ga masu shan tsanani saboda aikata adalci, domin Mulkin Sama nasu ne. (Mattiyu 5:10-12). Yayinda muka yi yaki na gaskiya mai kyau, akwai rawani na adalci wanda Mai Shari'ar mu a adalci zai bamu a ranar ta karshe, har ma ga waɗanda suke sauraron zuwansa. (2Timoti 5:7-8). Shan wahala da muke yi yanzu basu isa a misalta da ɗaukaka da aka keɓe mana ba; kada mu sa zukatan mu acikin wahala ba; mu bada gaskiya da Allah da Ɗansa . Ina gaya muku waɗannan saboda acikina kuna da salama. Acikin duniya kuna da wahala. Amma kada zuciyar ku ta ɓacce, na ci nasara da duniya"(Yohanna 14:1; 16;33).

## TATTAUNAWA

- Mu tattauna gaskiyan tsanatawa acikin ma'amalar mu da Krisiti. ( Ayyukan Manzani 16: 22-26)
- Idan bisa ga gaskiya ne, Mai Taimako (Ruhu) zai yi magana a maɗaɗin mu lokacin da kuke fuskantar kallubalai, ko a gaban alkalan na karya ko a lokacin da abu ya shafi rai da mutuwa. Mu tattauna dalilan da waɗansu Krisita suke neman Lawyoyi ko kuma

su yi karya domin su kuɓsuta daga masu zargin su.

- Yawan kashe kashe da raunan mutane, kori wadansu daga wuraren zamansu da hallakar da dukiyarsu wadannan suna raunana mutane wanda ya kai ga wadansu mutane sun canja adinin su. Mu tattauna karshen irin wadannan mutane game da samun ceto.
- Tsanatawa yana daya daga cikin muhimman abubuwan da zasu sa mu zama karfaffa acikin bangaskiya da kai ga kamalar ceton mu ne?
- Ta yaya Allah yake ceton mutanensa a lokacin kallubalai (Daniel 3:19-26, 6:16-23. Ayyukan Manzani 12:1-12.

## KAMALAWA

Tsanatawa ta zama daya daga cikin abubuwan da ta mane ma rayuwar wadannda suke rayuwa cikin Krisiti, amma daya a cikin abubuwan ban mamakin acikin wannan duka shi ne , Kullum yana bada hanya mafita daga cikin wadannan kallubalai duka. Yesu bai taɓa barin mu marayu ba ko ya yashe mu ba acikin kowane damuwa. Domin haka, bari mu bada gaskiya

## BINCIKE TA 14

# RAYUWAR MUTUMIN DA YA ZAMA KAFAFFE CIKIN KRISITI TA 1 Filibiyawa 3:10

## GABATTARWA

Saiwa wata ɓangare ne na itace da take girma a karkashin kasa kuma tana samu ruwa da wadansu sinadarin wanda take kaiwa sauran sassan itacen. Wannan tana nuna cewa girman itacen da bada yayan da zata yi ta dangana ne akan irin abubuwan da saiwar ta samu. Akwai wata hanyar rayuwan da mutumin da yake kafaffe acikin Krisiti ya kamata ya yi. Wannan hanyar rayuwan ta dangana ne akan irin abubuwan da mutumin ya samu ta wurin saiwar sa (Krisiti). Ina addu'a cewa zaka auna rayuwarka/ki akan sikeli ka gani ko kana bada yaya a matsayinka na mutumin da ka zama kafaffe acikin Krisiti.

## TATTAUNAWA

- Daga cikin wadannan ayyoyin, menene marmarin mutumin wanda yake kafaffe acikin Krisiti? ( Kolosiyawa 3: 10; 1Timoti 3: 15-17; Joshua 1:8, Wahayi Yahaya 1:3; Romawa 15:4; Zabura 119:15-16?)
- Ta yaya mutumin da yake kafaffe acikin Krisiti zai yi afani da maganar Allah? (yi afani da maganar Allah? (Yohanna 14:15; 8:31; Ayyukan Manzani 5:29; 1Yohanna 5:3; Ishaya 1:19; Luka 6:46?
- A gano daga cikin wadannan ayyoyin cewa mutumin da yake kafaffe acikin Krisiti yana kaunar ya yi zumunci da Allah, ba zai ɓoye a kalkashin zumuncin na jama'a duka ba (Mattiyu 6:5-8; 14:23; 1Thesalanikawa 5:17; Luka 5:16; Ibraniyawa 4:16; Filibiyawa 4:6-7; Kolosiyawa 4:2; 1 Littafin Tarihi 16:11)
- Ta yaya ya kamata mutumin da yake kafaffe acikin Krisiti zai yi rayuwa? ( 2 Korinthiyawa 5:7, Ibraniyawa 11:1; 6; 11; Yohanna 11:25-26; Markus 10:52; Romawa 1:17; Mattiyu 17:20?)

## KAMALAWA

Bisa ga tattauna da aka yi a cikin ayyoyin da suka gabata, mu koya cewa mutumin da yake kafaffe acikin Krisiti, mutum ne da ya sani maganar Allah, yana biyaya, addu'a da kuma wanda yake cike da bangaskiya cewa a wurin Allah, komai mai yiwo wa ne. (Mattiyu 19:26. Idan daya daga cikin wadannan abubuwan su kasa a cikin rayuwarka/ki ka sani ko ki sani cewa saiwarka ba kafaffe yake acikin Krisiti ba. Bari saiwar ka/ki ya zama kafafe kullum acikin Krisiti Yesu, Amin.

## BINCIKE TA 15

# RAYUWAR MUTUMIN DA YAKE KAFAFFE ACIKIN KRISITI TA 2 Filibiyawa 4:13

### GABATTARWA

A cikin wannan binciken, za mu kafa ido ne akan rayuwar mutumin da yake kafaffe acikin Krisiti ta wurin jimire tsanani kuma ya iya yin tsayaya da rashi a rayuwarsa. Za mu yi bincike kuma akan alamomi da hatsarorin zama Krisita tsaka tsaka da kuma yadda za'a iya zama kafaffe acikin Krisiti. A cikin duniyar da take cike ta kallubalai, rashin sanin gaibu da wahaloli, masu bi dole mu gane yadda zamu samu nasara acikin waɗannan matsalolin ta wurin kafa saiwarmu acikin Krisiti. Wannan binciken zata wayar mana da zurfafan gaskiya cewa zama kafaffe acikin Krisiti zata iza mu domin mu iya jimire tsanatawa da tsayaya da rashi. Zamu gano yadda tsayawa da karfi akan tushen Krisiti zata canja irin tunanin mu, ya bamu abubuwan na Ruhunaniya kuma ya sa mu ci nasara gaba da wahalolin.

Acikin tarihi duka, masu bins Yesu su fuskanci tsanatawa daban daban domin bangaskiyar su. Tun daga farkon Ikkilisiya har zuwa yau, masu bi su fuskanci gaba, wariya da kuma raunanawa domin tsayawarsu da mika kai da suka yi wa Yesu. Haka kuma, dayawa suka ɗaɗana lokuta na rashi abubuwa na biya bukatun su wanda ya gwada bangaskiyar su acikin tanadin da Allah za iya. Duk da haka, Littafi Mai Tsarki ta tabbatar mana cewa mutumin da ya zama kafaffe acikin Krisiti yana da karfi da sa zuciya domin ya jure tsanatawa kuma ya tsaya da karfi a lokacin rashi. Tare, zamu duba acikin Littatafai domin mu iya gano sharuɗa, alkawarai da kuma misalai da suka bayana wannan gaskiyan.

### TATTAUNAWA

- A wane hanyoyin ne rashi ko wahala za su iya kallubalanci bangaskiyar mu acikin Allah? Filibiyawa 4:6; 13; Yakubu 2:5, Nehemiah 8:10. Karin Magana 3:5-6.
- Ta yaya zama kafaffe acikin Krisiti zai iya taimakon mai bi ya jimire wa tsanatawa? Mattiyu 5:10-12; Yakubu 1:2-4; 2 Korinthiyawa 12:10; 1Bitrus 3:14. Romawa 8:35-37?
- Wane allamomi ne suke nuna cewa wannan Krisita mara zurfin sani ne ackin maganarsa? Ibraniyawa 10:25. Romawa 11:25, Markus 10:24; Mattiyu 19:14; Mattiyu 26:40-41; Mattiyu 23:5?

- Mene ne hatsarorin zama Krisita mai karamin sani? Mattiyu 13:20-22; Luke 6:49; Kolosiyawa 2:8; Afisawa 4:14; Galatiyawa 6:1?
- Mene ne mutum zai iya yi domin ya zama kafaffe acikin Krisiti? Yohanna 15:1-7; Afisawa 6:10-20; Mattiyu 16:24; Luka 14:25-34?

## KAMALAWA

Zama kafaffe acikin Krisiti tana nufi cewa rayuwarmu su kafu sosai acikin kaunarsa, alheri da ikonsa. Idan muna kafaffe acikin Krisiti, zamu iya yi tsayaya da tsanatawa mu iya jimirewa a lokacin rashi. Za mu iya zama da naciya a lokuta masu wuya domin mun sani tushen mu tabbatace take.

BINCIKE TA 16

# DAWAMEMEN SAKAMAKON DOMIN WANDA YAKE KAFAFFE ACIKIN KRISITI

**Yohanna 5:24; 6:33-35**

## GABATTARWA

Allah ya sani yadda zai cece mu da kuma lokacin da zai yi daga cikin gwaji na wannan duniya domin babu kayaswa ga waɗanda suke acikin Krisiti Ubangiji Yesu. Ta dalilin kasancewa acikinsa, mun zama sabobin halita., tsofofin al'amura sun shuɗe. Duba irin wannan baban sakamakon! Bugu da kari, labarin mai daɗin ji shi ne, yana addu'a domin al'majiraisa ko kuma masu bi domin Allah ya kubutar da su daga cikin yanayin da suka samu kansu aciki wanda ta zama dole ne su faru bayan an dauke shi zuwa cikin sama. Ba shaka mu ne hasken duniya, ba mu tafiya acikin duhu kuma ba. A matsayin mu na yayan haske, bari mu haskaka hasken nan namu domin mutane su gani ayyukan mu masu kyau sa'anan su baiwa Allah ɗaukaka. Yesu ya cece mu daga mulkin duhu kuma ya kawo mu cikin mulkin Ɗansa, ta wurinsa ne aka cece mu daga bautar zunuban mu.

Baiwar Ruhun gaskiya, wanda Yesu ya bamu, yana ci gaba domin ya falkas da Ruhun mu ya taimake mu acikin rashin karfin mu. Wasu lokuta, bamu sani mene ne zamu yi addu'a akai ba, amma Ruhu yana yi roko domin mu. A matsayin mu na yayansa maza da mata, Allah ya yi mana alkawali Mai Taimako (Ruhu Mai Tsarki). Yesu ba zai taɓa bari mu ko ya yashe mu ba. Hawaye da bakin cikin waɗanda aka daina hakin su, za'a share masu hawaye sa'anan kuma a saka masu da rawanin rai yayinda suke rayuwa acikin Krisiti Yesu. Ta wurinsa, an yantar da mu ba tare da wata shaka ba, gama an cece mu ba da abubuwan masu kawa kamar zinariya da azurfa ba, amma ta wurin jininsa mai tamani na ɗan ragon Allah.

## TATTAUNAWA

- Ta yaya muka tabbata cewa muna da gado a mulkin sama domin mu a rana ta karshe? Yohanna 14:1-4
- Ceton mu da farko ta nufe mu ne lokacin da ya zaɓe mu tun muna masu zunubi. Yanzu da mu masu bi ne, har yanzu muna da waɗanda za su rasa samu wannan Rai na Har Abada tsakanin mu ne? (Yohanna 15:16; 2Bitrus 2:9. Mu tattauna.
- (Mu ne yayan Allah maza da mata kuma magadan mulkin Allah. Wannan ɗaukaka ta nufa ayyukan mu masu kyau ne ko adalcin mu? ( 2Korinthiyawa 6:16-18; Galatiyawa 4:1-7)

- Mu tattauna tabbacin Rai Madawami acikin wannan tseren da muke yi na shiga cikin mulkinsa.
- Shin sakamakon na rai har abada za'a iya misalta shi da ladan tagula, zinariya da waɗansu kwafi da ake baiwa masu wasan tsere ko kolon ball a lokacin gasan su ne?

## KAMALAWA

Allah acikin madawamiyar kaunarsa da tausayin sa, bai yi lissafin kasawar mu ba, amma ya yi tunani irin sifar Ɗansa da aka yi mu da shi. Ya zabe mu, amma duk da haka bamu ɗauka matakin aiki akan hidimar ceton mu ba. An zaɓe mu kuma mu zama magadan Krisiti ko kuma mulkin sama. Magada tare da Yesu, tun lokacin da muke masu zunubi kalkashin ikon dakoki da zama bayi a kalkashin mulkin duniya. Ya cece mu zuwa ga zama yaya domin mu yayan sa ne, idan kuma yaya ne, magadan mulkinsa kuma. Galatiyawa 3:39, 4:1-7, ). Ɗaukaka ta tabbata ga Allah.

## BINCIKE TA 17

# SHIRIN SHAITAN DOMIN YA HANA MASU BI SU ZAMA KAFAFFU ACIKIN KRISITI

**Mattiyu 13:1-9; 18-23**

### GABATTARWA

Karfin kowace itace da irin yaya da zata bada ya dangana akan yadda saiwarta take da zurfi acikin kasa. Mai bi yana bukata ya yi girma ya zama kafaffe acikin Krisiti shi ne abinda Littafi Mai Tsarki ya jadada. Galatiyawa 4:1 ta sa muka gane cewa mudin magajin yana shi yaro ne, bai zama daban da bawa ba. Ba'a zama kafaFfe acikin Krisiti ba tana nuna zama rashin karfi da raunana acikin Krisiti domin iya fuskantar kallubalai na rayuwa. Iblis, tun farko yana ta aiki dare da rana babu fasawa domin ya gani cewa masu bi ba su yi girma acikin Ruhu ba. Yana yaki da Bishara sa'anan ya kirkiro abubuwan da za su janye hankalin mu a lokacin mu yau wanda su dauka gurbin marmarin sanin Allah sosai a rayuwar mu.

### TATTAUNAWA

- Mene ne ake nufi da hanawa? 1 Bitrus 5:8
- Shirin Iblis domin ya hana masu bi su zama kafaffu acikin Krisiti.
- Zai sa su yi zunubi (Farawa 3:1-7. Afisawa 2:2; Luka 22:31; Luk 22:3-5.
- Zai hana su iya yi addu'a, Mattiyu 26: 36-44)
- Zai hana su sa hankali akan jin maganar Allah
- Zai makanta idanun masu bi akan sanin gaskiyar maganar Allah.
- Zai janye hankalin masu bi zuwa ga bin abubuwan duniya maimakon abubuwan na Allah.
- A zamanin mu wane irin abubuwan ne Iblis yake afani da su domin hana mu zama kafaffu acikin Krisiti?

### KAMALAWA

A cikin binciken mu na yau, mun gane magabcin mu yana aiki babu hutu domin ya gani cewa yayan Allah ba su zama kafaffu acikin Krisiti ba. Ya yi nasara akan sa matasan wannan zamani su bi abubuwan na jiki. Amma Krisiti shi ne karfin mu acikin kasawar mu.

## BINCIKE TA 18

# HATSARORI DA KE TATARE DA RASHIN ZAMA KAFAFFE ACIKIN KRISITI GA MAI BI

**Kolosiyawa 2:6-7**

## GABATTARWA

Akwai bukatar duba "Hatsarori Da Ke Tatare Da Rashin Zama Kafaffe Acikin Krisiti Ga Mai Bi", yana da muhimmanci ga kowane mai bi musamman ga wanda yake kira kansa ya zama ɗaya daga cikin waɗanda za su cika alkawarin zama Mai Shaida Bishara. Wannan binciken zata bayana irin ilolin da suke tatare da rashin samu zurfafan dangataka da Krisiti, bisa ga kan magana na "Zama Kafaffe Da Ginanu Acikin Krisiti", kamar yadda aka jadaɗa acikin Kolosiyawa 2:6-7. "Kamar yadda kuka karbi Krisitio Yesu ya zama Ubangiji, saboda haka, ku yi tafiya acikinsa. Kafaffu ginanu acikinsa cikin bangaskiya. Kamar yadda aka koyar muku, kuna kasance acikinsa cikin bada godiya." A matsayin mu na masu bi, mun karbi Krisiti a matsayin Mai Cetonmu, amma tafiyarmu cikin bangaskiya bata tsaya anan ba. Dole ne mu cigaba da girma, muna balaga muna kafa kanmu da zurfi acikinsa. A wannan binciken, za mu bincika hatsarorin da zasu adabe mu idan mun yi watsi da wannan.

## TATTAUNAWA

- A tattauna albarkun da suke acikin zama kafafe acikin maganar Allah. Zabura 1:1-3, Farawa 39:3-6.
- A tattauna misalin mai shuki, kuma a faɗa mene ne kowane kasa take misalinta da yadda suke misalta hatsarorin rashin zama kafaffe acikin Krisiti?
- Bisa ga waɗannan wurare karatu a Littafi Mai Tsarki, 1Yohanna 2:15-17; Yakubu 4:4; Romawa 12:2; Mattiyu 6:19-21, a tattauna matsalolin da suke tatare da kaunar duniya.
- A tattauna hatsarorin rashin girma acikin Ruhaniya da rashin girma acikin sanin maganar Allah. Ibraniyawa 5:11-14; 1Korinthiyawa 3:1-3; Afisawa 4:13-14; 1Bitrus 2:2;
- Wane shawari wari ne aka bayar game da masu baudewa daga bangaskiya? Ibraniyawa 2:1, Kolosiyawa 1:23?

## KAMALAWA

A karshe, zama kafaffe acikin Krisiti ba abinda zai faru sau daya tak ba, amma rayuwa ce ta girma da zurfafan dangataka da shi Uhangiji Yesu. Yin watse da wannan muhimman ɓangaren bangaskiya zata iya kai ga sani abu bisa bisa, ya sa mutum ya zama da sauki duniya ta rinjaye shi, rashin girma acikin Ruhaniya, har ta kai ga faɗuwa daga bangaskiya. Yayinda za mu kamala wannan binciken, bari mu dukufa acikin ciyar da saiwar mu acikin

Krisiti, muna nazari akan maganarsa, kuma muna tafiya da aminci acikinsa, da sani cewa zamu samu karfi da natsuwa da muke bukata domin mu ci nasara akan hatsarorin da za su adabi bangaskiyar mu.

**BINCIKE TA 19**

# KRISTI A MATSAYIN GURBI

**Ibraniyawa 12:2; 13; 1Bitrus 2:21**

## GABATTARWA

Muna zuba ido ga Yesu, shi da yake shugaban bangaskiyarmu, da Mai Kamalata yana da muhimmanci idan muna so mu yi koyi da Krisiti a matsayin gurbi. Afisawa 5:1 tace, saboda haka, sai ku zama masu koyi da Allah, in ku kaunatattun ya'yansa ne. ku yi zama kauna kamar yadda Yesu ya kaunacemu, ya kuma ba da kansa dominmu, sadaka mai kanshi, hadaya kuma ga Allah. Yan'uwa, Krisiti ya sa Allah Uba da fari acikin rayuwarsa. Ya ce, bana nema in faranta ma kaina rai ba, amma in faranta wa wanda ya aiko ni. Domin mu yi koyi da Krisiti, dole mu bari komai duka, mu dauki gicciyenmu sa'anan mu bi shi. Dole mu yi biyaya da shi, muna bashi fiffiko ta wurin neman mulkinsa da adalcinsa da fari. Krisiti Mai Tsarki ne, ba shi da wani laifi cikake da gaskiya. Dole kai ma ka zama da tsarki, cikake kuma da gaskiya domin mu yi koyi da shi. Bai yi rayuwa munafurci kamar Mallaman Atawara ba, wanda su munafukai ne ta wurin zagayawa acikin tufaffin dogo masu kawa, suna kaunar gaida mutane a kasuwanai da kuma zama a wurare masu martaɓa cikin Majami'u da wurare sujada da wurare bukukuwa.

Krisiti ya damu da dukan mutane. Ba tare da nuna banbancin kabila, al'uma ko adini ba, ya nuna sahihiyar kauna mana. Ya ce mu kaunaci magabtan mu kuma mu yi addu'a domin masu tsanata mana. Domin ku iya yi koyi da Krisiti, dole mu nuna kauna wa mutane. Yesu ya yi addu'a ga Allah kada ya lissafta zunuban waɗanda suka kashi shi. Krisiti ya nuna kaskanci cikin yin hidima wa mutane. Zai yi kyau idan kai ma zaka samu Ruhun kaskanci. An kiraka domin wannan tunda Krisiti shi ma ya sha wahala dominka, ya bar maka gurbi domin ka bi acikin sawayensa. Bari a gan shi acikin rayuwarmu yayinda muke fama a wannan duniya yayinda muke yin koyi da Krisiti.

## TATTAUNAWA

- A tattauna Mattiyu 16:24 sa'anan a iya misalta shi da Yesu a matsayin gurbi.
- Ta yaya zamu bar Uba, Uwa, Ɗa da Ya domin Krisiti. Mattiyu 10:37-38
- Karanta Luka 20:45-47 Ko wannan wurin karatun ya tunashe ka akan wani mai addini da ka sani?

- An faɗa mana mu bi gurbin Krisiti. Krisiti da kaskanci. Krisita suna da kaskanci acikin siyasa, offis, kasuwanci da ikkilisiyoyi ne?

## KAMALAWA

A matsayin gurbi, Krisiti shi ne kaɗai wanda kowane mai bi zai nema ya zama kamarsa a rayuwa. Yana da kaskanci, baya daidaitawa, yana da karfin hali, Mai Tsarki da kuma cikake. Yana da tausayi ga yan adam ta wurin ciyar da su da warkar da su, yana cewa ku kaunaci magabtanku ku yi addu'a domin masu tsanata muku. Ya nuna rayuwar da ta cancanta a yi koyi da shi. Saboda haka, muhimmancin yin koyi da Krisiti ba sai a nanata ba. Bari Allah ya taimake mu domin mu cigaba da duban Yesu, muna maishe shi abu na fari acikin rayuwarmu. Amin.

**BINCIKE TA 20**

# DAYANTAKAR KRISITI DA UBA

**Yahaya 1:1-3; 10:30, Farawa 1:16**

## GABATTARWA

Bisa ga karatu da aka yi a waɗannan wuraren da aka lissafta, an gina,kyakyawan dangataka tsakanin mutane da Allah. Tun daga farkon shiri, hidima, gicciye, tashi daga matatu, da aikin alajibin hauwan Yesu Krisiti, dukan waɗannan suna nuna ɗayantakarsa da Uba. Yesu daidai yake da Uba acikin ayyuka, tunani da halita; Allah yana yin komai tare da sanin Yesu. Ba shaka shi ne dalilin da ya sa yace,"Bana yin komai don kaina, amma na Uba wanda ya aiko ni domin in aikata nufinsa ba nawa ba.Yahaya 1:1-3 tace, tun farko akwai kalma, kalma kuwa tare da Allah yake, Kalmar kuwa Allah ne, ta wurinsa aka yi komai. Yesu ya nuna kuma ya fada wa duniya cewa "Ni da Uba daya muke". (Yahaya 10:30); duk wanda yake kauna yana rayuwa acikin Yesu, Shi (Yesu) ma yana rayuwa acikin wannan mutumin kamar yadda Shi yana acikin Uba kuma Uban yana acikinsa.

Ɗayantakar Krisiti da Uban an bayana ma masu bi ta wurin Littafi Mai Tsarki. Babu wanda ya taɓa gani Allah acikinmu da ido. Duk da haka, Shi kadai, Ɗan wanda "Shi kansa Allah ne" kuma shi yana acikin dangatakar da ta fi kurkusa da Uba wanda ya bayana shi ga duniya. (Yahaya 1:18). Lokacin addu'ar Yesu domin masu binsa, Yesu da Uban babu wani abinda zai raba tsakaninsu ko rata a tsakaninsu shi ya sa ya yi adddu'a domin mu masu bi wanda Uban ya bashi mu zama daya kamar yadda shi da Uban su daya domin mu iya kai ga dayantuwa acikin dangatakarmu. ( Yahaya 17:20-23)

Saboda haka, Yesu babu shaka ya taɓa zukata da tunanin masu binsa da Kalmar rai, domin dukan abubuwan da ya yi kuma yana yi daga wurin Uban ne. Bugu da kari, idan kai mai bi, ka ji maganar ko ta wurin Yesu, ka rigaya ka ji daga wurin Uban kenan. Yesu, wanda shi ne baban matsakakanci, mai yi mana addu'a da kuma Allah mai jinkai, shi daidai yake da Allah.

## TATTAUNAWA

- Dangantakar Yesu Krisiti da Allah Uba za'a iya misalta shi da dangantakar mu da Ubanaimu da suka haife mu ne?
- A tattauna irin ɗayantakar Yesu da Uban bisa ga waannan ayyoyin Littafi Mai Tsarki. Yahaya 1:1-3; 10:30. Farawa 1:26.)
- A tattauna yadda muke rayuwa ta gaskiya acikin Krisiti Yesu bisa ga wannan magana "Duk abubuwan da suke na Uba, nawa ne" ( Yahaya 16:15)

- Wane darasi muka koya daga cikin dangatakar Yesu Krisiti da Allah (Uba)?

## KAMALAWA

Daga cikin bincikenmu yau, mu koya cewa mu ma daya muke da Uban ta wurin Yesu Krisiti matsakancinmu. Yayinda muke rayuwa acikin Krisiti Yesu, kuma shi ma yana acikinmu. Rayuwa idan ba tare da Allah ba, hatsari ne kwarai, kamar mai zama akan bom wanda zai iya pashe a kowane lokaci. Mutum ba zai iya ci gaba da rayuwa acikin wannan muguwar duniya da muke acikinta ta wurin dogara akan karfinsa ko karfinta ba. Saboda haka, muna bukata mu kasance tare da Allah.

## BINCIKE TA 21

# ZAMA KAFAFFE ACIKIN KRISITI

**Kolosiyawa 2:6-12**

**Ayya Haddacewa: Kolosiyawa 2:6-7**

"Da yake kun yi na'am da Aljasihu Yesu Ubangiji, to, sai ku tsaya a gare shi, kuna kafaffu, kuna ginuwa a cikinsa, kuna tsayawa da bangaskiya gabagaba, daidai yadda aka koya muku, kuna gode wa Allah a koyaushe.

## GABATTARWA

Allah bai cece mu domin mu zama bayin zunubi da Shaitan ba. Nufinsa da shirinsa domin mu shi ne mu girma mu yi balaga acikin Krisiti saboda kada a jujjuya hankulan mu nan da can ta wurin koyaswa daban daban. Zama kafaffe acikin Krisiti zai taimake mu domin mu san Krisiti mu iya mu mora mallakar mu a matsayin na yayan Allah ta wurin wannan binciken. Ina addu'a cewa Allah zai taimake mu domin mu kaffu acikin Krisiti.

## TATTAUNAWA

- Mene ne ka gane da wannan kalma "Ginane"?
  Bisa ga wadannan wuraren Karatun Littafi Mai Tsarki Kolosiyawa 1:28; 2:6-7. Yahaya 15:1-5, mene ne ka gane da "zama kafaffe acikin Krisiti"
- Ka auna daga cikin wadannan da aka lissafta yadda zamu zama kafaffe acikin Krisiti.
- Binciken Maganar Allah. (1Bitrus 2:2; Luka 10: 38-42; 2 Timoti 2:15; 3:16.
- Almajiranci: Mattiyu 4:18-19, Markus 3:14, Romawa 8:29
- Addu'a ba fasawa 18:1, 1Thessalanikawa, Ayyukan Manzani 2:42-43)
- Zumunci da Allah da sauran Yan'uwa (Ibraniyawa 10:25)
- Mene ne affanin zama kafaffe acikin Krisiti (Kolosiyawa 2: Mattiyu 28: Ayyukan Manzani 4:13. Yahaya 15:5)?
- Mene ne hatsarorin rashin zama kafaffe acikin Krisiti? Kolosiyawa 2:8; Afisawa 5:6; 1Korinthiyawa 3:1-4; Galatiyawa 4:1; 5:21b; 2Bitrus 1:9; Yahaya 15:6-

## KAMALAWA

Duk wanda bai zama kafaffe acikin Krisiti ba, yana acikin hatsarin samu hari daga zunubi. Shaitan da mutuntaka baza su shiga mulkin Allah ba. Hatsarorin rashin zama kafaffe acikin Krisiti suna dayawa kuma da sada. Ina addu'a cewa Allah zai sa ka zama kafaffe cikake acikin Krisit acikin Sunan Yesu. Amin.

**BINCIKE TA 22**

# KRISTI MAKIYAYI MAI KYAU

**Yahaya 10:11-14; Zabura 23:1-6**

## GABATTARWA

Makiyaye mutum ne wanda yake lura da dabobi. Mutum zai iya wannan a matsayin mai dabobin ko kuma a matsayin ma'aikaci. Yesu yace, "Ni ne Makiyayi Mai kyau." Dangataka da ke tsakanin masu bi da Krisiti yana kamar dangatakar da take tsakanin tumaki da makiyayi. Ubangiji makiyayinmu ne; mu tumakinsa ne. Krisiti ya karbe mu a matsayin kyauta daga wurin Uban, kuma babu wanda zai iya kwace mu daga hannun Uban.

Daya daga cikin hallaye masu kyau da ya sa Yesu ya zama Makiyayi Maikyau shi ne cewa yana malakarka kuma ba zai taba yasheka ba. Ya san tumakinsa kuma yana kiransu da sunayensu. Wannan shi ne daɗin bin Yesu. Ya san ka cikake, zai iya shugabance ka da kyau. Makiyaye Maikyau ya sani abinda kai (tumakin) yake so kuma zai iya baka abinda kake so a lokacin da kake so. Abu mai alfahari ne a ce kai na Ɗan Allah ne nugum. Krisiti ya damu da kai domin kai nasa ne. Ya maisheka ka zama nasa ta wurin biya da ransa, kuma ba zai taɓa yashe ka ba ko ya bar ka.

Wani abinda ya banbanta Yesu da zamansa na makiyaye maikyau shi ne cewa, yana kiyaye ka ya kuma baka rai na har abada. "Ina basu rai na har abada, kuma ba za su taba hallaka ba." (Yahaya 10:28). Idan Krisiti ne makiyayinka, ka samu kariya kuma ya baka kyauta mai tamani rai na har abada. Ta haka, ka samu tsira a hannuwan wannan da shi ke mai iko duka.

kisa, aka gicciye shi akan itace acikin tsananin walaha, dominka ne. Ya bada kansa da yardansa. Yesu ya kamala dukan abubuwan da ya zo ya yi su, kuma ya bada kansa ga mutuwa. Kuma shi ne abinda ya yi dominka a matsayinsa na makiyayi maikyau. Shi kadai ne ya iya aikata abinda ya cancanta domin a cece mutanen a kuma kuɓutar da mutanensa. Babu ko ɗaya wanda ya iya cika anabce anabce na Tsohon Alkawali, wanda yana nuna Mai Ceto da Makiyayin mutanen Allah

## TATTAUNAWA

- Ta yaya zaka gane idan kana ɗaya daga cikin tumakin Kristi? Yahaya 10:27.
- Ta yaya zai kawo mu a wurinsa ya kuma maishe mu tumakinsa? Yahaya 10:3
- Mene ne ya sa Yesu Krisiti ya zama mana "Makiyayi Maikyau?" Yahaya 10:11; Mattiyu 9:36
- Mene ne zai zama kamar abinda ake iya gani kullum a rayuwarmu na

bin Makiyayi Maikyau acikin duniyan da yake cike da kerkatai wanda suke kawo mana hari acikin tafiyarmu na bangaskiya? Mattiyu 16:24; Mattiyu 4:18-22.

## KAMALAWA

Muna bukata mu sani cewa Yesu shi ne Makiyayi Maikyau. Shi Allah ne cikake kuma zai iya tsare ya yi ma masu bi jagora dukan kwanakin rayuwarsu. Kamar yadda Makiyayi Maikyau yake tsare, ya kare sa'anan ya cece dabobinsa daga hari, Yesu shi ne yake yi mana wannan. Makiyayi kullum yana lura da tumakinsa, kuma Yesu yana kula da mu. Fiye da haka, Shi yana tare da mu kullum har matukar zamani kuma zai bi da mu dukan kwanakin rayuwarmu yayinda muke dogara gareshi. Littafi Mai Tsarki ya bayana Krisiti kamar Makiyayi Maikyau domin yana tsare, jagora, kuma ya ciyar ta wurin baiwa tumakin abinda suke so domin su yi girma acikin bangaskiya sa'anan a karishe ya bada ransa domin ya cece su daga hukunci.

**BINCIKE TA 23**

# DANGATAKAR DA KE TSAKANIN TUMAKI DA MAKIYAYI Yahaya 10:11

## GABATTARWA

Littafi Mai Tsarki yawanci lokaci yana amfani da misalin Makiyayi da kuma Tumaki domin ya bayana irin dangatakar da ke tsakanin Allah da mutanensa. Wannan kan magana zai duba wannan misalin cikake ya kuma duba abubuwan da suke faruwa. Da fari, tana da muhimmanci mu sani cewa wannan Makiyayin da ake misalin sa ba wai mutum ne mai lura da tumaki ba. She kuma mai karewa ne, mai bada abinci, kuma ya yi jagora. Yana kai tumakinsa inda akwai lafiya kuma ya tabata cewa suna da dukan abubuwan da suke bukata. Na biyun, tumakin acikin wannan misalin, yana nuna mutanen Allah ne. Suna dogara akan Makiyayin domin rayuwarsu da lafiyarsu. Ana kira su kuma su yi biyaya da umarnin Makiyayin su kuma su bi jagorancin sa.

Wannan misalin yana koya mana muhimman darasi akan dangatakarmu da Allah. Da fari, yana koya mana cewa Allah shi ne mai tsaron mu, mai biya mana bukata, da kuma jagora. Yana kaunar mu matuka kuma yana lura da mu sosai. Na biyu, yana koya mana cewa muna dogara akan Allah domin rayuwarmu da jin dadin mu. Muna bukatarsa ya jagorance mu ya tsare mu. Na uku, yana koya mana mu yi biyaya da umarnin Allah domin shi ya sani abinda ya fi mana kyau.

Acikin tattaunawa da za'a yi daga bisani, zamu duba irin dangatakar da ke tsakanin Makiyayi da Tumaki cikake. Zamu duba abubuwan da suke acikin wannan misalin domin rayuwarmu sa'anan mu koya yadda zamu yi rayuwa kurkusa acikin dangatakarmu da Allah.

## TATTAUNAWA

- Mene ne ake nufi idan an ce Yesu shi ne "Makiyayi Maikyau"? Yahaya 10:11-18
- Ta yaya dangatakar da ke tsakanin Yesu ya nuna irin dangatakar da ke tsakanin Makiyayi da Tumakinsa a cikin Tsohon Alkawali? Zabura 23:1-6, Ezekiel 34:11-16? Ana gani irin wannan tunanin Makiyayi a Ikkilisiyoyin mu yau?
- Ta wane hanyoyi ne Yesu yana lura da tumakinsa Mattiyu 11:28-30, Yahaya 14:6; 1Bitrus 5:7?
- Wane irin hanyoyi ne zamu iya mai da martani akan kaunar Yesu da

lura da yake yi mana? Yahaya 15:9-10, 1Yahaya 3:16; 1Korintiyawa 13:4-8?

Ta yaya zamu iya sa acikin ayyukanmu abubuwan da muka koya akan dangatakar Makiyayi Maikyau da tumakinsa a namu rayuwa? Afisawa 5:1-2; Filibiyawa 2;3-4. 1Bitrus 2:19-25?

## KAMALAWA

Dangataka da take tsakanin Makiyayi da Tumaki shi ne na kauna, yarda da biyaya. Makiyayi yana kaunar tumakinsa kuma yana lura da su sosai. Tumakin kuma sun yarda da Makiyayansu domin jagoransu da karesu. Kuma tumakin suna biyaya da umarnin Makiyayin domin su sani cewa yana da kyakyawan manufa dominsu. Bari ka cigaba da kasancewa acikin garken tumakin Yesu Krisiti dukan lokaci acikin Sunan Yesu. Amin

## BINCIKE TA 24

# RAYUWA DOMIN KRISITI TA 1

**Filibiyawa 1:21**

### GABATTARWA

Rayuwa domin Krisiti ta kunci ci gaba acikin kakarfan dangataka da haduwa da Krisiti, inda dalilin, abin izawa da manufar rayuwar mutum ta zama daya da shi. Wannan saudakar da kai ta wuce sanin sa kawai, tana kai ga mika rayuwar mutum wanda ta sa mutum ya yi domin iya yin zabe, ayyukansa da rayuwar da ta kai ga mika kai cikin bauta ma Krisiti. Irin wannan mika kai tana bayana irin bada kai da mutum ya yi wanda ta kunci koyaswa da misalin da Yesu ya bayar. Irin wannan rayuwa da ta kawo canji ta kunci hangen gaba ta ruhaniya inda ake gani mutuwa ba asara ba amma riba ce. Tana nanata irin zurfin bangaskiya acikin alkawalin rayuwar har abada da begen da ta wuce wannan rayuwa. Saboda haka, rayuwa domin Krisiti ta kunci mika kai gaba daya wanda ta shafi kowane ɓangaren rayuwa fara daga sharawa na kowane rana har zuwa abinda ya shafi rai da mutuwa.

### TATTAUNAWA

- Ta yaya mutum zai iya rayuwa domin Krisiti bisa ga waɗannan ayyoyin Littafi Mai Tsarki? Yahaya 3:3, 16; 11:25-26, Ayyukan Manzani 20:24; Romawa 12:1-21 Wahayin Yahaya 18:4-5?
- Mene ne afanin rayuwa domin Krisiti? Yahaya 3:16; Afisawa 1:7; Romawa 14:8; Ibraniyawa 13:5?
- Bukatan rayuwa domin Krisiti. Afisawa 2:10; 5:15-16; Mattiyu 5:16; Isaiah 60: 1-3?
- A tattauna hatsarorin da ke tatare da rayuwa don son kai. Galatiyawa 6:8; 5:19-21; Romawa 6: 23a; 8:6a; 12-13; Ezekiel 18:20; Wahayin Yahaya 21:8

### KAMALAWA

Yahweh yana buka mutane wanda da yardan kansu suka bari son kai, burinsu da jin daɗinsu saboda cewa Krisiti ya kasance acikinsu. Duniya tana cike acikin bakin duhu sosai kuma tana acikin bauta, tana marmarin jiran bayanuwar yayan Allah domin su nuna musu hasken da zai kubutar da su domin su samu yanci. Mu zubar da son kai domin nanmu su buya a cikin Kristi yayinda muke bayyana shi. Kolosiyawa 3:3.

Bari Yesu ya dauki shuganci a rayuwarmu.
Salama!

## BINCIKE TA 25

# RAYUWA DOMIN KRISITI TA 2

**Filibiyawa 1:10-26**

## GABATTARWA

Kamar yadda muka tattauna a binciken mu na baya, bimbini akan rayuwa domin Krisiti abu muhimmi ne a mawuyacin lokaci. A lokacin gurɓattacen rayuwa, cin gaba acikin cin hanci da rashawa, tsanatawa, da kuma jarabobi a koina acikin al'umma, ya zama dole Masu Bi su nemi bishewar Allah da jagorarsa sosai. Kalkashin jagorarsa, zamu iya fuskanci matsalolin rayuwa, muna koya mu yi rayuwar da zata nuna Allah acikinmu acikin kallubalai da al'umma ke fuskanta. Abin dubawa acikin wannan tafiya ta kunci tsarkake kanmu a matsayin kayan adalci muna ayyukanmu daidai da sharuɗan Allah. A matsayinmu na Masu Bi, akwai lokuta da za mu kai wanda rayuwarmu ya zama daidai da rayayyen hadaya, wanda ake gani a bagaɗin Allah. Wannan sahihiyar saɗaukar da kai ta kunci kowane ɓangaren rayuwarmu, tana shaida saɗaukar da kai domin rayuwar da ta bada kanta dungum ga Krisiti. Acikin bin wannan tsatsarkar saɗaukar da kai, addu'ar mu zata zama cewa kokarin mu ta zama abinda zai karfafa abinda muka yarda da karfafa bangaskiyar mu acikin Allah

## TATTAUNAWA

- A tattauna zahirin yadda rayuwa domin Krisiti zai taba rayuwar mu. (Mattiyu 4:19-22; 11:28, 2Timoti 3:12; Romawa 8:11-14; Filibiyawa 3:7-10; Galatiyawa 2:20.
- A nuna daga cikin waɗannan ayyoyin Farawa 39:2-12; 19-29, Ayyukan Manzani 5:27-29, 38-42; Ruth 1:15-18; Yahaya 6:5-12; Mattiyu 26:13. waɗannan mutanen da suka yi rayuwa domin Krisiti, mu nuna irin farashin da suka biya.
- A tattauna da gaskiya yadda Krisita zai iya yi rayuwa domin Krisiti acikin wannan wahalar tatalin arziki a lokuta faɗace faɗace da mugunta.

## KAMALAWA

Marmarin rayuwa domin Krisiti dole ta zama tare da kakarfan kudirin lissafin komai akan asara ne domin sanin Yesu da rayuwa dominsa. Allah yana acikin baban neman maza da mata waɗanda suna ashiriye domin su bada ransu a bagaɗin Yesu ba tare da wata shaka ba. Wannan ya rataya a kan irin waɗannan maza da mata da su yarda su kai Bishara har zuwa karshen duniya.

## BINCIKE TA 26

# MASHAIDIN KRISITI TA 1

**Ayyuka Manzani 1:8**

## GABATTARWA

Wannan aya tana ɗaya daga cikin umarnin na karshe da Yesu ya bayar ga Almajiraisa kafin ya hau bisa cikin sama. Ta kunci muhimmin alkawali da ya sa mutane aiki daga wurin Yesu zuwa ga mabiyin sa. Wannan alkawalin tana nuna irin ikon da Ruhu Mai Tsarki zai basu domin su iya aiwatar da aikin da aka basu yi ya zama da kyau. An sa Almajirai din acikin aikin shelar Yesu, suna bada labarin da faɗin abubuwan da suka ɗaɗana suka koya akan koyaswansa., mutuwarsa, da tashinsa daga matatu. Su zama shaiɗu akan ikon canja rayuwa da Bishara ya yi. Wannan alkawalin iko daga Ruhu Mai Tsarki ya wuce ace domin jin daɗin mutum shi kadai kawai; zata zama abin cika nufin Allah da Bishara a ko'ina a duniya

## TATTAUNAWA

- Menene ka gane da wannan kalman "Mashaidi"?
- Ta yaya ya kamata mu shaida Krisiti Mattiyu 5:16; Filibiyawa 2:5; Romawa 1:16; Ayyukan Manzani 13:5; 16; 25:32; 5: 30-32l Mattiyu 28:20?
- A tattauna bukata da ke akwai domin shailar Yesu (Markus 16:15, Ayyukan Manzani 1:4-5. 26:18; 10:43; Yahaya 15:16.
- Bisa ga waɗannan ayyoyin, a ina ne za'a shaida Krisiti? Markus 13:10; Mattiyu 28;18-20, Ayyukan Manzani 1:8; Irimiya 1:5;

## KAMALAWA

Yaweh yana neman mutanen da zasu tsaya a maɗaɗinsa ko'ina da kowane lokaci. Har yanzu yana bukata rayukan mutanen da basu tuba ba. Ka yi marmarin izawar Ruhu da ganga domin ka iya yi aikin da zuciyar Ubangiji yana akai, ka bada kanka ka yi magana. (2Timoti 4:2). Bari ka iya kai labarin Yesu zuwa kassashe duniya. Sallama!

**BINCIKE TA 27**

# MASHAIDIN KRISITI TA 2

**Ayyukan Manzani 1:8**

## GABATTARWA

Kamar yadda muka gani acikin binciken da ya wuce, waɗanda suka ɗaɗana ceto kuma suna cike da Ruhu Mai Tsarki an danka masu wannan aikin shaidar ikon Yesu mai canja mutane, wanda ya cece su ya kuma mayar da dangatankar da ke tsakanin su. Ana kira mu domin mu zama bakunan sa, Jakadunsa da wakilansa, muna nuna irin mutumen da yake wa duniya. Krisiti, wanda sau dayawa ana kiransa Hasken Duniya, ya zama ɓoyeye ga mutane idan bamu nuna haskensa ta wurin ayyukan mu da maganganun mu ba. Yayinda muna cikin wannan binciken, bari mu zama shaidun sa, muna nuna gabagaɗi ba tare da tsoro ba wannan hasken sa domin duka mutane su gani acikin sunan Yesu.

## TAMBAYOYI DOMIN TATTAUNAWA

- Fara daga Ayyukan Manzani 1:8; daga ina ne za mu fara yin shaidar Krisiti? Mene ne ya sa wannan yana da muhimmanci?
- Mene ne ake nufi da shaida daga Judea, Samaria da Duniya ya ke nufi? Ayyukan Manzani 1:8; da Mattiyu 28:18-20

  (i) A tattauna waɗannan mutane waɗanda suka yi shaida akan Krisiti a lokacin su da kuma yadda suka taɓa mutane.

  a. Almajirai (Mattiyu 28:18-20)

  b. Mutumin da aka haife shi makaho (Yahaya 9:13-15, 25b

  c. Ayyukan Manzani 9:22

  d.Maryamu Magdalene da wasu mata Markus 16:1-2, 9-11

  e. Yahaya 4:28-30, 39

  (ii). Ta yaya za mu iya yi shaida mu taɓa mutane kamar yadda suka yi?
- Mene ne abubuwan da za su hana yin shaida mai inganci ma Krisiti ( Ishaya 59:1-2, Ayyukan Manzani 19:13-19

## KAMALAWA

A zaman mashaidin Krisiti, zamu bayana shi ga kowane mutum saboda dukan mutane su zo wurinsa su san shi su ɗaɗana shi kamar yadda mu ma muka yi. Addu'ar mu shi ne mu zama rayayyun masu shaidar Yesu Krisiti ga mutanen da muke saduwa da su.

## BINCIKE TA 28

# KRISITI MATSAKANCI

**1Timoti 2:5-6; Ibraniyawa 9:15**

## GABATTARWA

Tun faduwar Ɗan Adam, masu zunubi sun kasa kusanci Allah in ba tare da Matsakanci ba. Littafi Mai Tsarki ta bayana wannan gaskiyan a hanyoyi dayawa, musaman ta wurin kafa Priesthood na Tsohon Alkawali. Kamar yadda muka gani, waɗanda suke rike da aikin matsayin Priest ne za su iya shiga wurin Mafi Tsarki a Haikali, in Allah ya nuna kasancewarsa ( Littafin Kidaya 3:5-10). Duk da haka, Littafi ma ta hakikance cewa waɗannan Matsakancin Tsohon Alkawalin daga karshe basu isa ba. Matsakancin Tsohon Alkawalin dole su yi hadaya domin zunubansu, wanda ya nuna cewa basu iya maganta matsalar zunubi gaba daya ba. Ko sadakokin da suka bayar, shi ma daga karshe basu isa ba. Haɗayan dabobi basu bada sahihiyar gafara ba., amma sune hanyoyin da Allah ya sa cewa zai iya gafarta zunubin yayan Israila ta wurin hakurinsa, da sanin cewa waɗannan zunubin, za'a kawar da su ta wurin hadaya da sulhu na Krisiti. Matsakanci, mai shiga tsakanin mutane biyu ne wanda kuma zai iya biyan bukatun mutanen duka biyu.

## TAMBAYOYI DOMIN TATTAUNAWA

- Bisa ga ganewarka, ka bayana aikin Matsakanci.
- Bayana yadda Krisiti ya zama Matsakanci mara-aibu ko laifi. (Romawa 3:25; 8:34; 1Timoti 2:5; Ibraniyawa 8:6; 15; 12:24; 9:15).
- A lissafta abububuwa akan Matsakanci mai kyau kuma a misalta shi da rayuwar masu bi a wannan zamani. Mene ne mahaɗin su kuma mene ne banbancin su . Farawa 18:22-32; 20:7; Littafin Maimaita Sharia 5:27; Levitikus 9:7; Ayuba 33:33?

  Krisiti ba ɗaya daga cikin hanyoyin da mutane za su nemi Allah ba. Shi ne kaɗai kofar. A tattauna wannan gaskiyan bisa ga waɗannan ayyoyin Littafi Mai Tsarki. Ibraniyawa 1:3. 3:1-6, 7:26-28.
- Ta yaya masu bi suka yi banza da Krisiti a wannan kwanakin. Yahaya 8:42; Ayyukan Manzani7:50-57; Zephaniah 1:1-6)?.

  A bada shawarwari hanyoyin da mai yiwu wa masu bi su yarda cewa Krisiti shi kaɗai ne Mastsakanci acikin kowane hali.

## KAMALAWA

Ta wurin mutuwar haɗaya mara zunubi domin dukan waɗanda suka bada gaskiya gareshi, Krisiti ya bada zarafi domin gafarar zunubi. Haɗayar da shi Matsakancin ya yi domin dukan mutane babu bambanci. Krisiti shi

kaɗai ne Matsakanci wanda muke da shi ko mu masu arziki ne ko talaka, maji ko mace, Sarki ko Bauwa. Acikin aikinsa na Matsakanci, Krisiti ya bada haɗayar kansa kuma yana addu'a domin mu. (Ibraniyawa 7:25)

## BINCIKE TA 29

# IKON SULHUNTAWA DA KRISITI YA YI

**2Korinthiyawa 5:17-21**

## GABATTARWA

Sulhuntawa shi ne mayar da dangataka acikin lumana bayan an samu jayaya ko gardama; ita ce ta kawo ganewa daga cikin rashin ganewa na mutane biyu. Sulhuntawa a wurin Krisita aiki ne na Allah ta wurin Krisiti wanda ta wurin wannan ne ya mayar da Ɗan Adam ga matsayin mai gamsuwa da kansa. Tun faɗuwar mutum a gonar iden, Allah ya yi Shirin sulhunta mutum da shi kansa. Hanya ɗaya tak da ta wurinsa ne mutum zai samu sulhu shi ne ta wurin zubar da jinni. Babu daba acikin dukan duniya nan wanda yake da jinni mai iko da zai kubutar da mutum daga dangatakar da ta yanke. Ta haka, Allah ya sa Yesu ya zama Ɗan Ragon haɗaya ta wurin jinkansa.

## TATTAUNAWA

- Mene ne Sulhuntawa ( Romawa 5:10?
- Mene ne ya sa mutum yake bukata sulhu? Romawa 3:23; 6:23; Farawa 3:8?
- Akwai wasu hanyoyin ceton mutum ne in ba ta wurin Yesu Krisiti ba? Ayyukan Manzani 4:2; Yahaya 14:6 Yahaya 6:44?
- Mene ne ake nufi da cewa an ɗanka mana hidimar sulhuntawa? 2Korintiyawa 5:19; Ibraniyawa 2:17-18

## KAMALAWA

Littafi Mai Tsarki yana cike da labaru maza da mata waɗanda suke ji daɗin jinkan Allah wanda ya sulhunta su da shi kuma da tsakanin mutum da dan'uwansa mutum. Yusufu ya yi jinkai domin ya bada zarafi domin sulhu da yan'uwansa duk da abubuwan da suka yi masa. (Farawa 37,41,42). Ɓataccen ɗa na Luka 15:11-32 ya sulhuntu da Mahaifinsa bayan da ya ɓarnatar da dukiyan Ubansa, wanda ya zama kusan ɗaya da albarkun mu acikin Krisiti Yesu. Bayan da muka ɗaɗana sulhu tsakanin mu da ikon Allah, dole mu ma, mu mayar da martani mai kyau.

## BINCIKE TA 30

# KRISTI SHI NE SHUGABAN BANGASKIYARMU DA KUMA KAMMALATA Ibraniya 12:2

## GABATTARWA

Yesu ɗaya yake da Allah, shi ne marubuci Littafi Mai Tsarki wanda ta wurinsa an bayana hanyoyin da za mu yi rayuwa. Yesu Krisiti ya fara wannan sabuwar hanyar rayuwa ta wurin zaman gurbin rayuwa da koyarwarsa, kuma ya kamala amencewa da muka yi da shi ta wurin tashinsa daga matatu. Yesu, wanda shi ne shugaban bangaskiyar mu da kamalata, tana nufi cewa Yesu shi ne ya fara shi ne kuma tushen bangaskiyarmu acikinsa, bayan da ya kafa tushen Krisitanci ta wurin rayuwarsa, mutuwarsa da kuma tashinsa daga matatu. Har ila yau, ana nufi cewa Yesus shi ya fara iza bangaskiyarmu, ya rayar da shi har ya kai ga kamala, wanda shi mai kamala bangaskiyar mu. Krisiti wanda shi ne kamalar bangaskiyarmu ya bamu kansa cikake saboda mu bada yaya ta Ruhaniya "Allah kuwa yana da iko ya ba ku fiye da bukatarku, domin kullum ku wadata da kome ta kowace hanya, kuma ta bayarwa hannu sake, kowane irin kyakkyawan aiki."

## TATTAUNAWA

- A tattauna yadda Yesu ya fara ceto da girma domin bangaskiya. Romawa 5:8-10, Ayyukan Manzani 4:12; Titus 3:5; Afisawa 2:8-9.
- A tattauna dalilai da suka sa dole mu dogara akan Krisiti a matsayin shugaban bangaskiyarmu da kamalata? Zabura 16:8; 73:26; 121:1-3; Yahaya 15:5; Romawa 8:8.
- A tattauna yadda bangaskiyarmu zata ingantu ko girma a matsayin na masu bi. Yahaya 1:12; 3:16; Joshua 1:8; Mattiyu 4:4; Yakubu 1:22.
- Karanta waɗannan ayyoyin Littafi Mai Tsarki Ibraniyawa 3:7-19; 4:1-11; 11:6; Mattiyu 21:22; Luka 1:37; Karin Magana 3:5 a tattauna waɗansu daga cikin affanin fansa da aka samu ta wurin Krisiti Yesu.

## KAMALAWA

Kyakkyawan ayyukan mu suna kama da irin abubuwan da Allah ya yi acikin mu ta wurin alherinsa, tare da amencewar mu domin ya gyara mu. Tun da Yesu ya fara kuma ya kamala bangaskiyar mu, dole mu yi tseren da kafa ido akansa. Da shi ne inda za mu fara kuma shi ne cikawar alkawarai. A wannan fani, kamalawa ba wai ya nuna karshen magana ba, amma a zama da sanin cewa ceto ya zama abinda kowa zai iya karba kyauta.

## BINCIKE TA 31
# KRISITI SHI NE TUSHEN EKKLESIYA
**1Korinthiyawa 3:11**

### GABATTARWA
Wannan aya ta jadaɗa aikin da Yesu Krisiti ne kadai ya zama jagaba da tushen bangaskiyar Krisitanci. Bangaskiyar Krisita ta ginu akan sa, babu wata tushe da zai maye gurbinsa ko ya kara akan aikinsa. A Tauhidin Krisita, an dauke Yesu shi ne ginshikin gini – wanda ta zama muhimmin abinda akansa ne dukan bangaskiyar mutane ya rataya. Shi ne tushen ceto, iko da wurin da za'a samu. Dukan ayyuka da koyaswa daga cikin Ekklesiya dole su fito daga wurinsa, gama shi ne mabubugan kasancewarta. Wannan tushen gaskiyan ta samo ambaci da Bitrus ya tabbatar akan Yesu cewa shi ne Krisiti, Ɗan Allah rayeye, ammbacin da Yesu ya tabbatar, da ya bayana niyar sa domin ya gina Ekklesiyar sa akan wannan gagarmar gaskiyan (Mattiyu 16:16-18). Bugu da kari, Yesu ya nanata hakin mabiyan sa domin su "yi kiwon Ekklesiyar Allah wanda ya pansa da jinninsa" (Ayyuka Manzani)

### TATTAUNAWA
- Daga cikin waɗannan Littatafai, a tattauna abinda ya sa Krisiti ya zama ginshikin Ekklesiya. (Afisawa 2:20; 1Bitrus 2:4; 6-7; Wahayin Yahaya 21:14; 1Korinthiyawa 3:10-11
- A tattauna irin yanayin Ekklesiyar da Krisiti ne kadai tushen ta. (Afisawa 2:19; 2: 4:1-16; 1Korinthiyawa 16:19
- A ambata a tattauna wasu daga cikin halayen Ekklesiyar da ba Krisiti ne tushen ta ba. Afisawa 4:18; 1Samaila 16:14
  Ta yaya abinda aka ambata a naba 3 a bisa za'a iya maganta shi?

### KAMALAWA
A karshe, bari mu zama da godiya ga Allah domin Yesu Krisiti, wanda shi ne kadai tushen wanda
ya kafa, kuma ga shaidu dayawa wanda ya ba mu na Allahntakar halinsa, tsarkakewar adalc'i, karban hadayarsa, yawan adduar roko da yake yi, da ɗaukakar mulkinsa mai zuwa. Bari mu gina bangaskiyar mu, bege, furci, biyaya da abinda muka koya akansa a matsayin tushen. Kada mu yi kamar muna rike da tushen indan ba ginni mu ke yi akai ba, gama tushe bata da wani afani idan ba ginni za'a yi akai ba. Da muka fara da tushen mai kyau, bari mu maida hankali cewa ginnin mu ta kunci abubuwan masu kyau sa'anan mu guje afanni da haɗahaɗen dukan abubuwa masu hallaka da iyakacen kokarin mu.

## BINCIKE TA 32

# MARMARIN SON KARA SANI AKAN KRISITI

**Filibiyawa 3:8-11**

## GABATTARWA

Wani ya fadi wannan da hikima cewa "Daya daga cikin mafi munin irin kuskuren mutum shi ne mutum ya manta da irin nasara da yake so ya samu. Wannan kuma gaskiya ne a rayuwar Krisita. Yana da sauki wani abu ya janye hankalin mutum ya manta. Ya kamata mu sani babu shaka kuma mu kafa hankalin mu kowane lokaci akan abinda muke nema. Addinin Krisita ba na dokoki da al'ada ba ne wanda dole mu yi kokarin kiyayewa domin mu hau matakala zuwa sama ba- maimakon haka, abu ne da ya shafi mutum da dangatakarsa da Yesu. Sanin Yesu bisa ga ganewar mutum shi ne ginshikin marmarin Krisitanci. Ta haka, sanin Yesu ba kawai amencewa da koyarwa magana a rubuce a takarda ba, amma cin gaba da ilimin sanin Krisiti a rayuwarmu. Shi ya sa sanin Krisiti a wurin Bulus ya zama abinda yake marmarin sa gaya. Tattaunawa da za mu yi yanzu zai yi mana jagorar bukatar mu na sanin Yesu.

## TAMBAYOYI DOMIN TATTAUNAWA

- Mene ne ake nufi da sanin Yesu
- A tattauna dalilin da Krisita yana so ya sani cikake akan Yesu. Yahaya 10:10; 14:6; 17:3; 1Yahaya 4:9.
- Sanin Yesu ya fi ace an san shi ta wurin ilimin kai kawai, amma sanin sa ya kunci samun dangataka da shi da kuma mika kai domin biyaya da koyaswansa.
- A tattauna yadda za'a bunkasa karfafan dangataka da Yesu. Irimiya 29:12-13; Yakubu4:8; Joshua 8:1.
- Wasu lokuta, marmarin sanin Yesu suna zuwa da kallubalai. A tattauna waɗannsu kallubalai ɗin. (Yahaya 15:20-25; 16:33)

## KAMALAWA

Yana da muhimmanci a san Yesu Krisiti a kuma so zama kamar shi. Wannan shi ne burin ka? Idan ba haka ba, kana bukata ka iza wannan marmarin sanin sa cikake domin ka zama kamar sa; zaka ga zarafi kewaye da kai da zaka yi aiki da shi. Zaka fuskanci jarabobi inda sai ka dogara ga ikon tashin sa daga matatu. Zaka fuskanci ɓacen rai inda kana bukata ka koya ka zama kamar shi a mutuwarsa. Ka ga waɗannan duka akan zarafi ne domin ka san Krisiti kuma ka tunashe kanka cewa wannan yana shiriya ka ne domin wancan baba rana lokacin da zai zo sa'anan za'a tashe ka acikin ɗaukaka tare da shi har matuka kuna tare. Wannan ita ce manufar mu.

## BINCIKE TA 33

# GINA JUNA ACIKIN BANGASKIYA

**Afisawa 2:20-22**

## GABATTARWA

Rugumar kanka a matsayinka na ɗan Allah tana samuwa ne da zato cewa zaka nemi zarafin haduwa cikin zumunci da saura Krisita, kamar yadda Bulus ya yi misalin sa acikin Afisawa. Wannan dangataka an nuna ta a hanyoyi biyu masu ma'ana. Da fari, kowane mai bi ana gani sa ne a matsayin muhimmin ɗaya daga cikin jikin Krisiti. Na biyu, mutanen Allah suna tasowa zuwa cikin zama tsatsarkar mazauni, wanda daidai yake da haikalin kasacewar Allah. Bisa ga Afisawa 2:20-22, wannan haikalin an ginata akan tushen Manzanai da Anabawa, tare da Krisiti Yesu da ya zama dutsen kusurwa. Ya jadaɗa cewa ana gina masu bi tare domin su zama mazaunin Allah ta wurin Ruhu a matsayin ɗaya daga cikin waɗannan hanyoyin. Domin mu iya kai ga balaga kuma mu cancanci zama mazaunin Allah, muna bukata mu ɗaukaka juna tare. Wannan tsari ana kiranta ingantuwar zuciya, kamar yadda aka jara ta a Afisawa 4:12. Bishara tana farawa da maye haifuwa, yayinda igantuwar zuciya tana sa girma cikin Ruhaniya. Manufar igantuwar zuciya ita ce, a kai ga balaga da zama kamar Krisiti. Idan kowane memba ya bada nasa gudumawa domin girman waɗansu acikin jikin Krisiti, dukan mutane za su girma, su bunkasa cikin lafiya da kuzari.

## TATTAUNAWA

- Ta yaya za mu gina juna Afisawa 4:29?
- A tattauna hanyoyin da za mu bautawa juna. Afisawa 4:32; Romawa 12:10; Filibiyawa 2:4; Galatiyawa 5:13
- A bayana yadda zama da dangataka da Allah tana da muhimmanci domin gina juna. Kolosiyawa 3:16
- Mene ne muhimman abubuwan na gina juna acikin bangaskiya.Romawa 12:15; 15:14; Galatiyawa 6:1-2; Mattiyu 18:19; 1Korinthiyawa 12:26?

## KAMALAWA

A karshe, a dukufa acikin taruwa kullum saboda inganta juna. Mutum ya tambaye kansa akan aikin Allah a rayuwarsa, bukatun da suke ci maka tuwo a kwariya da kuma hanyoyin da za mu yi wa juna hidima. Mu karfafa sadarwa a fili kuma a yi afani da wannan lokacin domin karatu Littafi Mai Tsarki, kada a boyewa juna kome, kuma a yi addu'a tare, ana nufa girma cikin Ruhu da hada kai acikin Krisiti. (Afisawa 4:13)

## BINCIKE TA 34

# GININ BANGASKIYA ACIKIN KRISITI

**Ibraniyawa 11:1; Luka 17:5**

### GABATTARWA

Bulus Manzo ya bayar da kyakyawan ma'anar bangaskiya da wanda aka fi sani cewa, "To, bangaskiya kuwa ita ce hakkakewar abubuwan da ake bege, a kai, ita ce kuma tabbatawar abubuwan da ba a gani ba." Bangaskiya acikin Yesu Krisiti shi ne amincewa da tabbatacen (1) Matsayinsa a zaman haifaffen Ɗan Allah, (2) kafara da ya yi domin zunubi da (3) Tashinsa daga matatu – kuma dukan wadɗanda muhimman abubuwa suna tabbatar mana. Bulus ya sa bangaskiya ɗaya daga cikin Ɗiyan Ruhu (1Korinthiyawa 12:9). Bangaskiya hakika tana zuwa ne ta wurin Ruhu, duk da haka kamar yadda Kamus na Littafi Mai Tsarki ta bayana. "Koda shike bangaskiya baiwa ce, dole a raya ta a bide ta har ya yi girma daga kankanin kwaya zuwa baban itace." Za mu iya yi abubuwa dayawa kuma mu iya rijayi mu faɗaɗa samun bangaskiya da muka karɓa ta wurin Ruhu Mai Tsarki.

### TATTAUNAWA

- Ta yaya mutum zai iya samu ceto? Romawa 3:23; 28, Galatiyawa 2:16)
- Ta yaya mutum mai bangaskiya ya kamata ya yi rayuwa? Galatiyawa 3:11; Mattiyu 4:4
- Mai bi zai iya yi girma acikin bangaskiyarsa (Luka 17:5; 2Bitrus 1:5-11; 2Thessalanikawa 1:3
- Ta yaya za mu iya gina bangaskiyarmu acikin Krisiti? 2Korinthiyawa 5:7; Zabura 119:16; Romawa 12:2; Ibraniyawa 12:28-29; Yahuza 1:20

### KAMALAWA

Bangaskiyarka acikin Krisiti zai iya yi girma da gaskiya yayinda kake nemansa kowane rana kuma kana aikata nufin Allah. Bangaskiya, tuni ta rigaya ta zama maka sharuɗan aiki acikinka, zata zama maka kuma sharuɗan iko. Bangaskiya ba shaka tana zuwa ne ta wurin Ruhu Mai Tsarki, duk da haka, kamar yadda Kamus na Littafi Mai Tsarki ta bayana shi, "Koda shike bangaskiya baiwa ce, dole ne a rayyar da ita a kuma neme ta har ta yi girma daga karamar kwaya zuwa baban itace."

**BINCIKE TA 35**

# EKKLESIYA JIKIN KRISITI NE TA 1

**Kolosiyawa 1:18-19**

## GABATTARWA

Yesu Krisiti shi ne "Kai" jiki, wanda ita ce Ekklesiya., sa'anan "membobin"jikin ana ganin su kamar Ekklesiyar. Ekklesiya iyalin Allah ne, haikalin Ruhu Mai Tsarki ne, Tsatsarkar al'umma, kuma jikin Krisiti. Ekklesiya a matsayin jikin Krisiti wata muhimmin kalma ce ga masu bi kuma hanya mai kyau ne na ganewar bayanuwar kaunar Krisiti ga mabiyan sa. Idan membobin Ekklesiya ana ganin su kamar jikin Krisiti, sa'anan ne Ruhun Krisiti zai iya kashe ayyukan jiki ya kuma gicciye tsohon mutumin daga duka ayyukan jiki. A matsayin Ekklesiya, Yesu shi ne ya zama cikakken gurbi da Allah ya sa a gaban mu, dole mu bi sawayensa a matsayin mu na zama jikinsa. Saboda haka, dayantuwar masu bi a matsayin Ekklesiya tana da muhimmanci. Dole mu yi la'akari da abubuwan da suke gaba da mu domin su janye hankalin mu daga kafa ido akan Krisiti ya zama da wuya. Abinda Bitrus ya ɗaɗana akan tafiya da ya yi akan ruwa (Mattiyu 14:25-31) ɗaya daga cikin misalai yada za'a iya janye hankalin mu daga wannan tafiyar mu ta ruhaniya.

## TATTAUNAWA

- Mene ne yake sa Ekklesiya ta zama jikin Krisiti? Afisawa 4:15-16
- Idan Ekklesiya jikin Krisiti ne, mene ne ya sa waɗansu mutane suna tsamani Ekklesiya na Pastor ne? 2Korinthiyawa 12:13-20?
- Akwai banbanci ne tsakanin jikin Krisiti da Ekklesiya? A tattauna bisa ga waɗannan ayyoyin. Kolosiyawa 1:18, 1Korinthiyawa 12:13; 27-13;
- Krisita ta Karnin 21st tana darajanta Ekklesiya a zaman jikin Krisiti ne? A tattauna bisa ga 1Korinthiyawa 5:1-4; 9-13

## KAMALAWA

Allah yana so Ekklesiya ta yi rayuwa kamar Krisiti domin ita jikinsa ne domin duniya ta iya karanta ta, ta ji ta, ta ganta ta kuma sani cewa Krisiti da gaskiya yana rayuwa acikin Ekklesiya ( Mu ne membobin jikinsa).Ta yin haka, duniya zata  zo kurkusa da ceto da kubuta. Idan muna bukatar mu yi tafiya a sawayen Krisiti a matsayinmu na membobin jikinsa kuma mu ɗaɗana rai a yalwace, dole ne mu yi kokarin zama kafaffe acikin Krisiti.

## BINCIKE TA 36

# EKKLESIYA JIKIN KRISTI NE TA 2

**1Korinthiyawa 12:12-31; Afisawa 4:11-13**

## GABATTARWA

Ekklesiya ta fuskanci damuwoyi da kallubalai daban daban tun farkon kafawar tasa. Mun fara da banbance banbance acikin ra'ayoyi akan Bisharar Krisiti. (1Korinthiyawa 1:10-13). Rarabuwa acikin Ekklesiya ba sabowar abu ba ce; kabilanci da wariya sune suka fi yawa. Banbancin dariku sun rigaya sun ci karfin Ekklesiya. Amma abin tambaya shi ne: Don mene ne? Wannan yana nunawa cewa jikin ba ɗaya ba ce kuma? Mu tuna, tunda muna da baye baye daban daban bisa ga alherin da aka bamu, bari mu yi aiki da su bisa ga haka. Mu jiki ɗaya ne, gama ta wurin Ruhu ɗaya, dukan mu an yi mana baptisma cikin jiki daya.

Saboda haka, a matsayinmu na Ekklesiya, bari mu yi kokari mu gina jikin Krisiti har dukan mu mu kai dayatuwa cikin bangaskiya da ilimin sanin Ɗan Allah tunda muna da alherin da aka ba mu, kowane bisa ga bangaskiyarsa da hidimarsa (1Korinthiyawa 12:12-31). Idan mu membobi jikinsa ne, dole ne mu yi rayuwa iri ta Krisiti. An fara kira masu bi Krisiti a Antioch domin rayuwarsu ya kama da na Krisiti; amma abu takaici yau shi ne cewa mutane dayawa suna ce su Krisita, amma rayuwarsu bai yi zama daidai da rayuwar Krisiti ba.

## TATTAUNAWA

- A tattauna kallubalai da Ekklesiya a matsayinta na jikin Krisiti ke fuskancta a wannan Karnin ta 21st.
- Mene ne yake kawo wariya a Ekklesiya yau duk da cewa mu jiki ɗaya ne? (1Korinthiyawa 1:10-13)
- Ta yaya jikin zata iya yi tsayaya da kallubalai na ciki da na woje (Kolosiyawa 3:15; Afisawa 4:4; 15-16?
- A tattauna irin tunanin mutane akan zama Ekklesiya a matsayinta na jikin Krisiti. Yahaya 2:19-22
- Ta yaya zaka iya misalta membobin Ekklesiya yau a zaman jikin Krisiti bisa ga waɗannan ayyoyin Littafi Mai Tsarki. ( 1Korinthiyawa 12:25-26; Afisawa 4:15-16; 4:25; 5:29-30.

## KAMALAWA

Idan za mu yi tsayaya da wannan lokacin mu yi rayuwa kamar Ekklesiya, dole ne mu bunkasa zurfaffan kauna da dangataka kut da kut da Krisiti,

kuma kalmarsa ta kaffu sosai acikinmu. Idan mun samu kallubalai ra'ayoyi daban daban, za mu iya ci nasara akan su domin shi wannan baban NI NE shi ne tushen mu. Allah yana sa zuciya akan mu a matsayin jikinsa domin mu iya cikata sharuɗan mulkinsa.

**BINCIKE TA 37**

# BISHARAR TA GASKIYA

**Romawa 1:16**

## GABATTARWA

Rinjaye da Bishara take da shi kada ta zama na bada bege ga masu zunubi kadai ba, wanda zai sa su gani kamar ceton Krisiti ya zama na alheri kyauta kawai ba, alhali kuma suna cin gaba acikin saɓawa dokokin Allah. A lokacin da hasken gaskiya ya haskaka tunani mutum, kuma mutum ya gane irin yawan zunubansu, sa'anan ne za'a samu sakewa. Zai canja rayuwarsu, suna zama masu biyaya ga Allah ta wurin samun karfi daga wurin Mai Ceton sa'anan su yi rayuwar sabon hali da tsabtan rai. Manufar Bishara shi ne ya sa mutum ya bunkasa cikake acikin tsarkaken kauna ma Allah da rayuwar rashin son zuciya da kauna ma juna.Wannan kaunar ta fi gaba da nuna halin kirki ko taimako, tana fitowa ne daga cikin zuciya tsarkake daga dukan rashin adalci. Bishara, yadda Allah ya bayana, tana nema ta ɗaga Ɗan Adam daga zunubi zuwa adalci. Waɗanda suka rungume Bishara suna ci gaba da bidi abubuwan Ruhaniya da naciya da dogara akan ikon Mai Cetonsu. Zukatansu ya zama mazaunin Ruhu Mai Tsarki yayinda suke shailar ɗaukakar wanda ya kira su daga duhu zuwa cikin haske mai ban mamaki.

Bai isa a shaida dsa baki cewa an bada gaskiya da Bishara ba; amma tsarkakewa ta wurin Bishara tana da muhimmanci. Idan ba tare da nasara akan zunubi ba, shaidar bakunan mu bata da amfani. Kayayuwa da aka yanke ta amma ba'a cire ta daga saiwar ba, zata sake tohu da hankali, har ta fi karfin ruhun mutum. Yayinda zamu shiga cikin tambayoyi da tattaunawa, bari Ubangiji Allah ya ba mu ganewar gaskiyan Bishara. Amin.

## TATTAUNAWA

- Ta yaya Littafi Mai Tsarki ta bayana Bishara. Romawa 6:1-16; 2Korinthiyawa 4:4; 1 Timoti 1:11?
- Bisa ga waɗannan ayyoyin Littafi Mai Tsarki Romawa 5:16; 8:7; 2Kor. 5:18-19; 21; Kolosiyawa 1:20-21, mene ne dalilin ceto?
  Wane irin yaya ne Ruhu zai haifar acikin waɗanda suke biyaya da Bishara. Galatiyawa 5:22-23; Zabura 92:14; Yahaya 15:5; Romawa 7:4; Afisawa 5:9; Filibiyawa 1:1; Kolosiyawa 1:10?
- Ta yaya Bulus ya bayana kiyayarsa akan koyaswan da tace Krisita za su iya ci gaba acikin zunubi? Romawa 6:1-2, Romawa 6:15; Galatiyawa 5:13; 1Bitrus 2:16; Yahuza 4?4?
- Ta yaya Ekklesiya ta farko suka ci nasara akan wa'azin Bishara (Kolosiyawa 1:23; Ayyukan Manzani 8:4?

## KAMALAWA

An bada yalwataccen tabbaci ga waɗanda suka tsaya acikin biyayarsu ga Allah. Wannan alkawalin ta bayana cewa idan ka ci gaba da nacciya ba tare da bauɗewa acikin bangaskiya ba, ka zama da tushe da natsuwa, kuma ka yi tsayaya ba tare da ka janye daga begen Bishara ba, shi Mai Pansa zai mika ka da tsarki, ba tare da tabo ba, kuma mara abin zargi a gaban Allahnsa. Wannan tabbacin ta zama abin sa gagarmar tushen bege ma Krisita, wanda ta fi kome acikin duniya nan, yayinda su tsaya daram suna sauraron yayan sakamakon alkawali wanda Bishara ta bayar.

## BINCIKE TA 38

# IKON KRISITI

**Luka 10:19; Afisawa 1:20-21**

### GABATTARWA

Yesu Krisiti yana da iko wanda babu wani da yake da shi a sama da duniya duka. Abinda zai iya yi ya fi tunani mutum ko abinda za'a iya tambaya, kuma yana da iko ya ci nasara akan abubuwa duka ma kansa. A zamansa na Alllah a cikin jiki, Ɗan Allah, ne ya yi alajibai, alamu, da abin ban mamaki, baban daban, kuma ya tashi daga matatu. Wannan shaida ne akan Allahntakar sa. Mazaunin mu a sama take, kuma muna marmarin jiran Mai Cetonmu, Ubangiji Yesu Krisiti, wanda, da wurin ikon da ya sa kome a kalkashinsa, zai sake wannan kaskantaccen jikunan mu ya zama kamar nasa jikin. An baiwa masu bi gagarumar kyauta – iko, acikin sunansa domin yin addu'a da nuna iko, wanda zai sa kowane magabci ya rusuna masa. Yau, muna ammence da muhimmancin ilimi, duk da haka ikon da yake acikin sunan Yesu shi ne yake kawo canja rayuwa, ba wai kawai ilimi ba. (2Timoti 3:15). Lokacin da hasken Krisiti ya bayana akan rayuwar masu bi, muhimman abubuwa suna faruwa. Muna kafa ido ne akan ikon Ruhaniya, wanda ta fi dukan irin ikoki.

### TATTAUNAWA

- Wane irin ganewa kake da shi akan ikon Krisiti yau? (Kolosiyawa 1:17; Mattiyu 8:27; 1Korinthiyawa 1:24?
- Ta yaya zamu iya yi afani da ikon da muke da shi acikin Yesu Krisiti (1Korinthiyawa 1:24; Filibiyawa 3:10; Afisawa 1:19; 1Bitrus1:5?
- A tattauna ikon Allahntakar Krisiti a waɗannan ayyoyin: a. Kafara. b. Tashin matatu. c. Warkaswa Filibiyawa 3:10; 1Kor. 1:18; Ibraniyawa 1:3; Mattiyu 10:1; Yahaya 2:19-21; Luk 5:17
- A bincika irin alkawarai da aka yi ta wurin ikon Krisiti domin waɗanda suka bada gaskiya. Markus 16:17-18; Mattiyu 10:1; Yahaya 10:20-30; Ibraniyawa 7:25; Afisawa 5:14),
- A tattauna bayanuwar ikon Krisiti a zuwansa na biyu. Masu bi na karnin 21 suna shiriye ne? Markus 13:26; 2Bitrus 1:16; Yahaya 5:25-26).

### KAMALAWA

Idan Krisiti ne ya zama tushen bangaskiyar mu, mun ɗanka mashi ranmu domin ya yi rayuwarsa acikinmu kuma mun karbi shugabancinsa a rayuwarmu. Yayinda muke raguwa, Krisiti yana karuwa. Baban manufar kowane ɗayan mu shi ne mu samu rai wanda yake boyeye gabadaya acikin Krisiti, inda mu dogara acikin ikonsa da zai canja mu ya yi mana jagora.

## BINCIKE TA 39

# TAMMANIN KO FARASHIN ZAMAN ALMAJIRIN KRISITI Luka 14:25-27; Mattiyu 16:24-26

## GABATTARWA

Wannan kalman "Tammani" ko "Farashin" tana tunashe mu a zaman mu a Nigeria irin kallubalai da muke fuskanta domin biyan bukatun mu na rayuwa. Tamani ta kunci wahaloli da matsalolin da suke tatare da cikata ayyuka, ko waɗanda waɗansu suka sa mu yi ko kuma waɗanda yanayin rayuwa ne suka sa mu – na jiki, ta tunanin mu ko kuma ta Ruhaniya. Ta fanin Ruhaniya na ɓangaren almajiranci, tamani ta wuce irin ta tatsuniya; wannan fadakarwa ce ta gaskiya. Almajirai Yesu suna fuskanci kallubalai haɗa kansu da shi, gogormayar da ta shafa zamanai. Yesu ya gane cewa waɗanda suke bi kakkausan hanyar sa dole ne su zama ashiriye domin mutum ya musunci kansa, wata jigo ne a wannan tafiya, wannan tana bukata mika kai wanda Yesu ya bayana daladala. Almajirai zasu iya fuskanci kiyaya da tsanatawa domin rayuwarsu tare da Yesu, amma waɗanda suka jimire za'a albarkace su da rai na har abada bayan da suka ci nasara akan duniya. Jin daɗin duniya nan tana kallubalanci rayuwar mu ta Ruhaniya, tana janye hankalin mu daga hanya. Kauna duniya da jin dadin ta, ba za su haɗu da bauta ma Yesu ba. Kira domin mutum ya ɗauki gicciyen sa ya bi Yesu umarni ne na shiga cikin duniya domin shaida Bishara ma dukan duniya, Duk da kallubalai ɗin,an tabbatar wa masu bi kasacewar Yesus kullum, wannan yana nuna halin tausayin Allah Uba. Kodashi ke, wahalar da muke fama da su yanzu ta zama kamar babu idan mun kwatanta da ɗaukaka da take jiran mu. Ana karfafa masu bi mu yi naciya tare da bangaskiya, da sanin cewa nasara ya zama nasu acikin sunan Yesu.

## TATTAUNAWA

- A bincika wahalolin da suka fuskanci mutanen da rayuwarsu na almajiranci, Mattiyu 26:69-75; 27:3-5; Ayyukan Manzani 5:1-11).
- A bincika shawarar Yesu akan malakar duniya da ya zama kallubalai ma masu bi acikin dangatakarsu tare da shi. (Markus 10:16-26
- A shiga cikin muhimmancin musun kai a matsayin kakkausan halin da za'a auka acikin dangatakar almajiranci Mattiyu 16:24-26
- A lissafta kallubalai da ake fuskanci kullum acikin rayuwar na almajiranci.)

## KAMALAWA

Kallubalai da suke gwada bangaskiyar mu a matsayin na almajirai suna dayawa., duk da haka muna samun karfafa zuciya da sanin cewa Yesus ya biya tamann akan gicciye. Babu ma abinda za'a misalta da shi banbancin da ke tsakanin abinda muke fuskanta da abinda Krisiti ya jimire. Saboda haka, hakin mu shi ne mu yi tseren ba tare da shakan bangaskiya ba, muna kafa ido akan abubuwanda suke a sama kamar yadda Littatafai Masu Tsarki suka fada.

## BINCIKE TA 40

# KRISITI: ALKALI MAI ADALCI

**Mattiyu 7:1-5; Romawa 2:16**

## GABATTARWA

Acikin kaunarsa mara iyaka da tausayi, Allah ya yi tanaɗi hanya mara wuya domin zaɓɓaɓun mutanensa su kai ga ɗaukakar alkawali ba tare da sharia mara adalci a duniyan da take cike da shariar nutane inda shari'ar karya zata iya ci saboda rashin iya ganowa sosai inda akwai kasawa. Allah, acikin hikimarsa, ya sa Yesu Krisiti mai shariar adalci. Ba kamar alkalan mutane ba, Yesu Krisiti baya sharia da nuna banbanci ko danginsa ba, amma da adalci da aka danka masa daga wurin Uban. Rayuwar adalci ana iya bayana shi ta wurin ammenci. (Habakkuk 2:4). Yesu ya jadaɗa yadda ana bukata adalci domin shiga cikin mulkin sama, wanda ya wuce irin na Farisiyawa da mallaman Attaurat (Mattiyu 5:20). An kudurta ma adalai su gaji rai na har abada, wannan gaskiyan Yesu ya misalta shi da yardansa ta wurin karban sakamakon ayyukan mu a gicciye (1Bitrus 3:18). Yesu, alkali mai adalci, yana aunawa ba ta wurin yadda ake gani a woje ba, amma da adalci, yana sakaya daidai ga mabukata da matalauta.

Saboda haka, ana gargaɗi masu bi kada su sharanta bisa ga abinda ake gani kawai ba, amma su yi sharia daidai (Ishaya 11:4; Yahaya 7:24). Ba shaka lokaci ya kusato da asirai za'a bayana su, kuma sharia zata fara, da mutanen Allah. A wancan ranar, alkali mai adalci nan zai zo acikin adalci, yana sharianta matatu da rayayyu bisa ga ayyukansu. (2Timoti 4:1; Wahayi Yahaya 20:12)

## TATTAUNAWA

- A bincika dalilai da ya sa waɗansu Krisita suna yi shariar karya akan ƴan'uwan su masu bi yayinda su ma suna aikata irin zunuban da yan'uwansu suke yi. (Mattiyu 7: 1-5)
- A yi nazari akan dalilai da ake samu rashin adalci acikin sharia tsakanin Mallaman addini ko Pastorci da membobi.
- A bincika sabani tsakanin Yesu, alkali mai adalci wanda yake bincike ayyukan cikin zukatan mutane da halin boye ayyuka mara kyau ga mutane.
- Ka yi nazari akan naka yadda kake sharanta da kuma sasanta rashin jutuwa tsakanin mutane. Kana sharanta daidai ne ko kuwa bisa rashin adalci?

## KAMALAWA

Bari mu daina sharanta mutane bisa ga yadda muke gani a woje, kuma maimakon haka, mu yi sharia cikin adalci da gaskiya. Yesu, alkali mai adalci, yana sane da boyeye da ayyukan da suke a fili, yana tabbatar da sharia daidai. Kamar yadda ya dauke nauyin hadaya doming gafarar zunubi, bari mu kubuta duka daga yin shariar mara adalci acikin sunan Yesu.

## BINCIKE TA 41

# ITACEN INABI NA HAKIKA

**Yahaya 15:1-16**

## GABATTARWA

Domin a gane muhimmancin wannan kalman "Itacen Inabi Na Hakika", bari mu kawo misali daga fanin noma. Manomi yakan ɗauka lokacinsa ya gyara gonarsa, ya nome ta, ya sa ruwa, ya nome ciyawa, ya gyagyara domin ya tabbatar da samu afanin gonar. A wannan misalin, kowane itace mai bada yaya ana ɗauke shi a matsayin itacen gaskiya acikin gonar ko a filin. Yesu Krisiti, bisa ga Littafi Mai Tsarki ana kiransa nunan fari ko kuma haifuwar fari kafin sauran halita, shi cikake. Itacen Inabi na gaskiya, mu ne kuma rassan na wannan itacen inabin mai bada yaya. Allah yana a matsayin mai gonar da kuma manoma, wanda ya sa a yi noma wanda zai bada yaya. Itatuwan da ba za su bada yaya ba, za'a sare su, amma itacen inabi na gaskiya, ana sake gyara ta domin ta samu isashen abinda zai sa ta kara bada yaya. Zaman mu kafaffe acikin wannan itacen inabin zai nuna irin karfi da muke da shi. Idan bamu kafu sosai acikin Krisiti Yesu ba, ba za mu iya shaida Bishara ba kamar yadda ya jadaɗa acikin Kalmar sa, "idan ku kasance acikina, ni kuma acikinku, zaku tambaye kome ne ne kuke so, kuma za'a yi muku.

Masu bi suna bukata ciyarwa babu fasawa acikin rayuwarsu. Mai bi na gaskiya yana bada yaya mai kyau kuma rayuwar su a bayane take ta wurin ayyukan su. (Mattiyu 7:19-19. Rayuwa mai kyau daidai yake da itace da aka dasa a bakin ruwa, tana bada yaya koyaushe, wanda gayanyen ta ba zata yi yaushe ba. (Zabura 1:3-4. Kasancewa acikin Krisiti Yesus yana da afani domin bada yaya wanda ya cancanci irin kira da aka kira mu da shi

## TATTAUNAWA

- A bayana yadda kamar rassan itacen inabi mai kyau, masu bi suna iya bada yaya da zai dawama har abada ta wurin tsarkakewa. Yahaya 15:1-2, 16
- Mu duba misalin itacen da aka dasa a bakin ruwaye da kuma rassan Itacen Inabi na gaskiya da ba su bada yaya ba. (Zabura 1:3-4; Yahaya 15:5-7.) Mene ne dalilai da irin haka zata faru?
- A tattauna hatsarorin da rayuwar Krisita mara bada yaya yake aciki (Zabura 1:4; Mattiyu 7:19; Markus 11:12-14)

## KAMALAWA

Kokarin mu na iya yin wani abu mai kyau har da bada yaya, rayar da ita, jagoranta, da kuma kareta, ya dangana ne akan muna da Yesu acikin rayuwarmu. In ba tare da shi ba, ba za mu iya yin kome ba. Rayuwa da tsoron Allah tana gayawa duniya cewa mu masu bin Yesu Krisiti ne. Abinda aka ɗanka mana shi ne mu shiga cikin duniya mu almajirantar da al'umma ta wurin shaida Labarin Mai Daɗi da mutane mabukata (Mattiyu 28:19.) Yayinda muna yin haka, muna kawo ɗsaukaka da sunan sa a nan duniya.

**BINCIKE TA 42**

# IDAN BA TARE DA NI BA, BA ZAKU IYA YIN KOME BA Yahaya 15:1-11

## GABATTARWA

Wannan magana mai karfi na Ubangijinmu Yesu Krisiti da ya taɓa mutane cewa, "Idan ba tare da ni ba, ba za ku iya yin kome ba." Kafaffe acikin Bisharar Yahaya, ta musaman sura 15, aya 5, waɗannan kalmomin suna kawo mana gaskiya mai zurfi ta wurin misalin itace da rassan ta. Wannan kwatanci tana bayana dangataka da ta wajaba tsakanin mai bi da Krisiti. Itacen da misalin rassan tana biɗa mu duba zurfin dogararmu akan Allah. A duniyar mu da tana fifita gwanitar mutum da isawar sa, Yesu yana kallubalantar wannan ta wurin furta wannan gaskiyar ta fi karfin al'adu da dabi'un mutane. Kasancewa acikinsa ba wai shawara ba ne, amma muhimmanin abu ne acikin rayuwarmu na Krisita acikin wannan tafiyar. Ana kira mu gane cewa karfi na gaskiya, manufa, da aiki tana fitowa ne daga zurfaffan dangataka da Yesu Krisiti. Yayinda za mu ci gaba da wannan binciken, za mu gano yadda za mu iya cikin ayyukanmu mu kasance acikinsa kullum kuma mu ɗaɗana ikon canjawa da taɓa rayuwarmu acikin dangatakarmu na kut da kut da shi.

## TATTAUNAWA

- Mu auna muhimmancin zaman Yesu Itacen na Hakika da kuma masu bi a matsayin rassan. Yahaya 15:1-2
- Mu bincika hatsarorin da ke tatare da rashin kasancewa acikin Krisiti. Yahaya 15:4-6
- Mu yi bimbini akan dukan ɗiya Ruhu Mai Tsarki da kuma matsalar rashin samu wannan a rayuwar mai bi. Galatiyawa 5:22-23
- A tattauna mahaɗin da ke tsakanin kasancewa acikin Krisiti, bada yaya, da kuma ɗaɗana cikkaken salama Yahaya 15:8-11

## KAMALAWA

Yayinda za mu shiga cikin binciken kalmomin Yesu mai zurfi a Yahaha 15, bari mu rungumi gaskiyan cewa ba za mu iya yin kome indan ba tare da shi ba. Bari binciken mu ya kai mu ga samun karfi, manufa, da kuma gamsuwa cikin kasancewarmu acikin Krisiti, muna bada yaya wanda za su daukaka Allah Uba, kuma mu ɗaɗana farin ciki daga cikin zurfaffan dangatakarmu da Ubangijinmu.

## BINCIKE TA 43

# BUKATAR KASANCEWA ACIKIN RAYUWAR WANDA YAKE KAFAFFE ACIKIN KRISITI

**GABATTARWA**

**Yahaya 15:4-5; Galatiyawa 2:10**

Zama kafaffe acikin Krisiti ita ce tushen bangaskiya, amma kasancewa acikin rayuwarsa tana rayar kuma tana wadatar da tafiyarmu na masu bi. Kasancewa kullum acikinsa, ba zaɓi ba ne, amma dole ne. Yayinda zama kafaffe acikin Krisiti yana daidai da dasa gaggarmar itace, kasancewa acikin rayuwarsa yana kama da zama a kalkashin inuwar itacen, kana ɗaɗana wadatar kasancewarsa wanda yake sarafa rayuwarmu. Tafiyar mu acikin Krisiti tana farawa ne da karɓan Krisiti a matsayin Ubangijinmu da Mai Cetonmu, wanda ya kafa tushen bangaskiyarmu. Duk da haka, rayuwa kafaffe acikin Krisiti abu ne da yake ci gaba da girma kuma rayuwa ce na mika kai har iyakar kwanakinmu. Wannan kasancewar tana karfafa bangaskiyarmu kuma tana kai ga cikawarmu da godiya. Kasancewa acikin rayuwar Krisiti ita ce samun mafaka da kariya acikin kasancewarsa, muna sa fifiko akan abubuwan ta samaniya akan abubuwan na duniya. Tattaunawa da za'a yi daga bisani tana nuna muhimmancin bukatar zama kafaffe acikin Krisiti kullum ga waɗanda suke kafaffe acikin rayuwar Krisiti, kuma mu gane ikonsa na canja rayuwarmu.

**TATTAUNAWA**

- Mene ne ake nufi da "kasance" ko kuma "zama" acikin Krisiti, kamar yadda aka bayana acikin Yahaya 15:4-5
- Mene ne ya sa Yesu ya yi afani da misalin itace da rassan domin ya bayana wannan ra'ayin na kasancewa acikinsa?
- Bisa ga wannan aya (Zabura 91:1), mene ne sakamakon kasancewa ko kuma zama acikin rayuwar Krisiti?
- Ta yaya rayuwar wanda yake kafaffe acikin Krisiti ya zama daban da mutumin da yake rayuwa domin kansa (Galatiyawa 2:20?

**KAMALAWA**

Zama acikin rayuwar wanda yake kafaffe acikin Krisiti ta kunci ci gaba ta wurin zaɓi da ganga a kasance acikinsa da kuma rayuwa ta wurin bangaskiya acikinsa. Yayinda za mu kasance acikin rayuwar Krisiti, namu rayuwa zata canju, zamu kuma bada yaya na kasancewarsa acikinmu. Wannan ba abu zaɓi ba ne, amma ya zama dole domin girma cikin Ruhaniya da kuma zama da afani a zaman mu masu bi. Wannan zaɓi da muka yi na kasancewa acikinsa, rayuwa bisa ga bangaskiya, kuma mu sa zukatanmu da tunanin mu akan abubuwan samaniya tana kawo mu acikin cikkaken dangataka da zamu ɗaɗana na wadatar kasancewarsa.

**BINCIKE TA 44**

# MUHIMMANCIN KASANCEWA DA RUHUN GANEWA ACIKIN ZAMA KAFAFFE 1 Yahaya 4:1

## GABATTARWA

Kafawar tushe mai karfi acikin bangaskiya tana da muhimmanci acikin tafiyar kowane mai bi. Wannan tushen tana bukata cikakken dangataka ta ruhaniya da kuma marmarin iya ganewa abubuwan na ruhu. Zama kafaffe tana kunce da zama da ruhun ganewa tsakanin ruhohi da banbanta tsakanin gaskiya da karya, ta ainihi da ta karya, kamar yadda aka nanata acikin Mattiyu 7:15.Daya daga cikin abubuwan da suka kunci ganewa ita ce ammencewa da gaskiya, wanda ta zama muhimmi acikin tabbatar da gaskiyar mutum (1Korinthiyawa 2:12-13; Karin Magana 2:3-5). Har yanzu kuma, tana karfafa abinda muka yarda, tana taimaka ma masu bi su haɗa bangaskiyarsu ta wurin banbanta tsakanin abinda ya zama daidai da bangaskiyarsu da abinda ya musunta shi. (Ibraniyawa 5:14. Bugu da kari, ruhun ganewa tana iza mutum ya guji jaraba da nasara sosai. Tana tabbatar cewa zaɓe da aka yi ta zama daidai da bangaskiya da shi da kuma dab'u, suna taimaka a zama da halin zama kafaffe da kuma mutuncin dabi'a. (Filibiyawa 1:9-11; Romawa 12:12) Ruhun ganewa kuma tana taimako domin ɗauka shawara, ta yi jagorar zabi da ta zama daidai da sharuɗa ruhaniya (1Sarakuna 3:9; 4:29). Gina sahihiyar dangataka tsakanin al'aummar masu rayuwar Ruhu ita ma wata muhimmin abinda za'a samu ta wurin ruhun ganewa. (Zabura 119:66) Wannan mahaɗin tana bada taimako, karfafawa da kuma taimakawa cikin girma tare, wanda zai taimaka a zama da halin zama kafaffe acikin sa.

## TATTAUNAWA

- Mene ne ake nufi da zama da ruhun gane ruhohi? Ta yaya wannan baiwar ruhu ta shafi tafiyar mu acikin bangaskiya? ( 1Korinthiyawa 12:10)?
- Ta yaya ruhun ganewa ya zama da muhimmanci domin zama da karfi da kuma kafaffe acikin bangaskiya? (Afisawa 6:11-12)
- A tattauna lokuta acikin Littafi Mai Tsarki da waɗansu mutane suna bukata ruhun ganewa Mattiyu 4:1-11; Ayyukan Manzani 16:16-18)
- Ta yaya za mu iya zama da ruhun ganewa acikin rayuwarmu? Wane hanyoyin da zamu dauka daladala domin mu karfafa wannan baiwar? (Ibraniyawa 5:14)

## KAMALAWA

Gane Ruhohi tana da muhimmanci acikin tafiyarmu ta bangaskiya. Tana

taimakon mu gujewa ruɗani, mu zama kafaffe acikin bangaskiya, kuma mu samu jagorar Ruhu Mai Tsarki. Domin mu iya ganewa tsakanin abinda yake na Allah da abinda ba na Allah ba, zamu iya zama kafaffe da zurfi acikin Krisiti, karfafa bangaskiyarmu, mu yi tafiya acikin hasken gaskiyar sa. Saboda haka, mu nemi jagorar Ruhu Mai Tsarki kuma mu zama kafaffe acikin sahihiyar maganar Allah mara canjuwa.

**BINCIKE TA 45**

# MATSAYIN AUNA KAI GA WANDA YAKE KAFAFFE ACIKIN KRISITI 2Korinthiyawa 13:5

## GABATTARWA

Auna kai ya zama ɗaya daga cikin jigajigan abinda kowane mutum wanda yake kafaffe acikin Krisiti zai yi. Zai zama da afanin acikin reno da zurfafa dangatakar ka da Yesu, ya kuma sa ka yi girma, da tabbatar da rayuwar da ta zama daidai da sharuɗan Krisita. Bari mu duba matsayin auna kai sosai ga wanda yake acikin Krisiti: Auna kai zai sa masu bi su yi tunani akan tafiyarsu acikin bangaskiya, zai taimake mu domin mu tatance gaskiyan bangaskiyar mu, ya tabbatar cewa da gaskiya mu zama kafaffe acikin Krisiti ba wai mun koya abinda addini ta ce ba (2Korinthiyawa 13:5).

Yana kai mu da ganewa da zunubi a rayuwarmu waɗanda ba daidai suke da nufin Allah ba. Ya kan iza mu yi tuba da shaida zunubanmu, wanda su cacanci zama da dangataka na kut da kut da Allah ( 1Yahaya 1:9). Mai bi wanda bai damu da wannan auna kai kullum ba zai karasa yana tsere ne kawai ba tare da sani cewa yana akan hanya ko baya akan hanya ba, yana ayyuka ne kawai ba tare da bada yaya ba.

## TATTAUNAWA

- Mene ne ya sa auna kai yana da muhimmanci ga waɗanda suke kafaffe acikin Krisiti? Mene ne ake nufi da "auna kai" kamar yadda aka ambata acikin 2Korinthiyawa 13:5; Makoki 3:40?
- Wane wasu afani ne ke akwai acikin auna zukatanmu da ayyukanmu bisa ga bangaskiyar mu? Zabura 139:24.
- Acikin Zabura 139, Dauda ya gayyaci Allah ya duba ya sani cikin zuciyar sa. Mene ne zamu iya koya daga cikin wannan faɗin gaskiya da kuma tuntube da zamu iya yi acikin dangatakarmu da Allah?
- A tattauma wannan ra'ayin "komawa wurin Allah" kamar yadda aka ambata acikin Makoki 3:40. Ta yaya auna kai zai iya taimake mu zuwa kurkusa da Allah?
- Ka bada labarin abinda ka ɗaɗana a lokuta da auna kai ya taimaka ga girma cikin Ruhu ko kuma samu canjawa a rayuwarka
- Akwai sananen abubuwa ko kallubalai da mutane suke fuskanta lokacin da suke kokarin auna kansu bisa ga bangaskiyarsu? Ta yaya za'a ci nasara akan wannan?

## KAMALAWA

Auna kai ba abinda zai faru rana ɗaya ba, amma abinda zai ci gaba ana yi ga waɗanda suka zama kafaffe cikin Krisiti. Tana zama kamar madubin ruhaniya, yana taimaka domin mutane su yi girma, zurfafa bangaskiyarsu, sa'anan su zama kurkusa acikin dangatakarsu da Yesu. Ta wurin auna kai, masu bi, zasu iya daidaita ransu da nufin Allah kuma su ɗaɗana ikon canjawar Ruhu Mai Tsarki.

## BINCIKE TA 46

# KU KAFA IDANUNKU AKAN ABUBUWAN DA SUKE A SAMA

**Kolosiyawa 3:1-2**

## GABATTARWA

Kolosiyawa 3:1-2 ta yi magana mai karfi, tana umarci masu bi su "kafa tunanin su akan abubuwan da suke a sama, ba abubuwan duniya ba." Wannan aya ta kunci zurfafan koyarwa Krisita, tana kallubalatar masu bi domin su bada fifiko ga abubuwan ruhaniya fiye da na duniya. Acikin wannan binciken Littafi Mai Tsarki, za mu dubi muhimmancin kafa tunaninmu akan abubuwan da suke a sama, muna binciken abubuwan da ake yi a fili acikin rayuwarmu kullum da kuma sanin irin yadda ya taɓa rayuwar bangaskiyarmu a wannan tafiya.

## TATTAUNAWA

- Mene ne ake nufi da kafa tunani akan abubuwan da suke a sama, kuma ta yaya wannan tunanin ya banbanta da irin ta duniya? (Kolosiyawa 3:1-2)
- Don mene ne Krisita za su bada fifiko akan abubuwan na sama akan muraɗin duniya da burinta, kuma ta yaya wannan zaɓen ya taɓa halin mu da ayyyukan mu? (Mattiyu 6:19-21; Filibiyawa 3:19-20)?
- Wane iri wasu hanyoyi da muka sani zamu iya zama da tunanin za zuciyarmu akan abubuwan da suke acikin sama acikin rayuwarmu kullum, kuma ta yaya zamu iya gujewa daukar hankalinmu da kayan duniya da abubuwan da ba za su dawama ba? (1Timoti 6:17; Romawa 12;2)
- Ta yaya kafa tunaninmu akan abubuwan da suke a sama zata rinjaye dangatakarmu da mutane, har ma da masu bi da marasa bi? Kolosiyawa 3:12-14, 1Yahaya 3:16-18

## KAMALAWA

Umarnin kafa tunani akan abubuwan da suke a sama , sharuɗan rayuwa ne domin Krisita. Sa tunaninmu da burinmu su zama daidai da hakikanin gaskiyar abubuwan na samaniya tana iya canja halinmu, ayyukanmu da dangatakarmu. Irin wannan tunanin tana iza mu masu bi mu yi rayuwarmu da ma'ana, da mutunci da bangaskya mara jijiguwa, muna samu bege da wadar zuci acikin alkawarai na Allah. Yayinda zamu sa waɗannan koyaswa acikin zuciyarmu, zamu iya ratsa cikin kallubalai na rayuwa da alheri da taɓa mutanen duniya da suke kewaye da mu ta hanya masu kyau.

## BINCIKE TA 47

# MATSAYIN HIDIMA DA ZAMA KAFAFFE ACIKIN KRISITI

**1 Samaila 3:1-11**

### GABATTARWA

Allah yana bukata cewa mutum ya zama mai aiki acikin gonarsa bayan da an cece shi, ya sami ceto. Ya kira mutum domin aiki tare da shi da ikon Allahntakarsa saboda ya sa nufinsa da shirinsa anan duniya. Amma wannan tana bukatar mutumin wanda yake ashiriye domin a yanke waɗansu abubuwa a rayuwarsa, a tsarkake shi, kuma ya shiga cikin zurfafan dangataka da Allah domin ya iya yin wannan aiki mai daraja. Littafi Mai Tsarki ya ce, a baban gida, akwai kayan aiki dayawa, waɗansu domin aikin ɗaukaka, waɗansu kuwa don kaskantaccen aiki. (Timoti 2:20-21). Yawan mika kanka domin dangatakar na kurkusa da Ruhu Mai Tsarki, haka kuma zaka zama da amfani sosai acikin hidimarka ma Allah.

### TATTAUNAWA

- A tattauna abubuwan da ake bukata mutum yana da su domin yin hidima . Romawa 12:1; 1Samaila 15:22; 1Samaila 3:9; 1Korinthiyawa 3:1-3; Kolosiyawa 4:12; Ibraniyawa 5:14; 2Timoti 2:20-22, Mattiyu 9:36 da 2Timoti 2:15.
- Mene ne hatsarorin baiwa mutumin wanda bai zama kafaffe acikin Krisiti ba aikin yi? 1Timoti 3:1-6, 1Korinthiyawa 13:11; Mai Hadishi 10:16, Galatiyawa 4:1-3.
- Wane irin kayan aiki ne Allah yana zato za mu zama? 2Timoti 2:20-21, Markus 2:22
- Allah yana bukata cewa mu yi girma da zurfi cikin tafiyar mu da shi. A tattauna wannan bisa ga waɗannan ayyoyin Littafi Mai Tsarki. Mattiyu 13:5; Luka 5:4-11

### KAMALAWA

Samaniya kullum tana neman mutanen da za su nuna kamanin Krisiti a duniya. Wannan zai zama mai yiwo wa ma waɗanda suka gina tafiya da Allah babu fasawa kuma suka yarda da kansu su yi tafiya mai zurfi tare da Alllah kullum. Muna rayuwa acikin duniyan da mutane suna so su yi hidima a bagaɗi amma a zahirin gaskiya, ba su samu horaswa domin wannan aiki ba.

Ubangiji ya bamu marmarin shiga cikin zurfafan tafiya tare da Allah kullum.

## BINCIKE TA 48

# BIN SAWAYEN UBANGIJI

**Yahaya 14:6**

### GABATTARWA

Yesu yace, "Ni ne hanya, ni ne gaskiya, ni ne kuma rai. Ba mai zuwa wurin Uba sai ta wurina." Bin Yesu ya wuce furci bada gaskiya da baki kawai, yana bukata mu sa bangaskiyarmu acikin aiki da kuma yin rayuwarmu ta zama daidai da koyaswarsa. Acikin wannan binciken, zamu duba zurfafan maganan bin sawayen Ubangiji, mu shiga cikin hanyoyin wanda Yesu ya yi rayuwarsa da kuma gano yadda zamu iya sa koyaswarsa su kai mu ga rayuwar da zamu cika nufinsa da ma'ana acikin namu rayuwa.

### TATTAUNAWA

- Mene ne ake nufi da bi Yesu? Yahaya 14:6; Yahaya 12:26; Mattiyu 16:24?
- Wadanene wasu daga cikin hanyoyin da Yesu ya yi rayuwarsa? Mattiyu 11:29; Filibiyawa 2:3-8; 1Bitrus 2:21-25)?
- Ta yaya zamu iya sa koyaswan Yesu acikin namu rayuwa? Mattiyu 7:12; Mattiyu 22:37-39.
- Wane kallubalai ne muke fuskanata domin bin Yesu. Mattiyu 10:34-39, 2Timoti 3:12, 1Bitrus 4:12-19
- Ta yaya zamu iya taimaki juna acikin bin Yesu? Ibraniyawa 10:24-25; Galatiyawa 6:2; 1Korinthiyawa 12:12-27?

### KAMALAWA

Bulus Manzo gabagaɗi ya umarci waɗansu domin su bi gurbinsa yayinda yake bin gurbin Krisiti (1Korinthiyawa 11:1). Yesu ya zma masa gurbin mai kyau da zai bi, kuma muna bukata mu yi hatara idan za mu ɗauka mutum, ko sananun masu wa'azi kada su maye gurbin Ubangiji. Bari mu iya samu alherin da zamu yi tafiya acikin sawayen Yesu Krisiti, wanda shi ne gurbin mu cikakke.

BINCIKE TA 49

# KA TSARE AL'AMURAN KA

**1 Timoti 4:16**

## GABATTARWA

Acikin 1Timoti 4:16, Bulus Manzo ya shawarci masu bi da "su tsare al'amuransu". Wannan magana a takaice tana rike da zurfafan muhimmanci acikin koyaswan Krisita, tana nanata muhimmancin tsayawa da karfi, da kuma zama da tsaro ta ruhaniysa. Wannan aya tana karfafa yin biyaya da zama karfaffe da ginane acikin Yesu Krisiti, zama karfaffa acikin bangaskiya, da yalwata acikin godiya. Ta zama kamar tuni domin a yi lura, kana tsare abinda ka bada gaskiya akai da ayyukanka daga samu damuwa daga woje wanda za su iya sa ka bauɗe daga koyaswan Krisiti.?

## TATTAUNAWA

- Mene ne Bulus yake nufi da ya gayawa Timoti cewa "kula ko maida hankali"?
- A tattauna gagarɗin kada a dauke su zuwa bauta talala. Kolosiyawa 2:8; 2Korithiyawa 11:3-4)
- Mene ne ikon da ke kawo canji acikin bangaskiya? Romawa 12:2; Galatiyawa 5:22-23)
- Mene ne hakin Ekklesiya acikin tsare bangaskiyar mutum? Ibraniyawa 10:24-25; Yakubu 5:16

## KAMALAWA

Kolosiyawa 2:6 tana bada hikima da ta wuce kaiɗeɗen lokaci, tana umarci mutane su tsare bangaskiyarsu da hallayensu. Wannan shawara ta nanata muhimmancin zama kafaffe acikin Krisiti da kuma zama a faɗake akan abubuwan da za su iya rinjeye ka. Kira na "tsare al'amuranka" tana a matsayin hanyar jagora, wanda tana sa Krisita su yi tsayaya sosai, suna neman su banbance, su kafa zurfafan rassan acikin bangaskiyarsu. Wannan kudirin tana kai ga rayuwar da zata dubi kanta a madubin koyaswa da kaunar Yesu Krisiti.